# HIKIMAR ZIYARAR KABURBURAN WALIYYAI

**Wallafar: AyatulLahi Sheikh Ja’afar Subhani**

**Fassarar: Yunus Muhammad Sani**

**Dubawar: Hafiz Muhammad Sa’id**

# Ziyarar Kaburbura Masu Daraja

Da Sunan Allah Ta'ala Mai Rahama Mai Jin Kai

Tsira da amincin su kara tabbata a bisa Manzon rahama Manzonmu Annabi Muhammad amincin Allah Ta'ala ya kara tabbata a gare shi da iyalensa tsarkaka

Makabarta wani wuri ne babba a cikin birni da kauye Wanda yake kunshe da matattun mutane marasa rai wanda yake dauke da babba da yaro mai iko da talaka daga magabata wadanda suke cikin barci mai zurfi da yake kamar ba za a farka ba.

Ziyartar wannan wuri Wanda yake nuna gajiyawar dan Adam, sannan kuma yake da rawar da yake takawa wajen gusar da duk nuna iko ko kwadayin abin duniya ga mutum. Yayin da mutum mai hankali ya ga wannan wuri mai ban tsoro, zai fahimci rashin tabbatuwar duniya daga kusa, sannan ya fara tunani a kan mafita sakamkon fahimtar manufar halittar duniya da ya yi. Kuma zai sanya ya fita daga cikin magagin dimuwa da son kai, sannan ya fara tunanin neman abin zai taimaka masa wajen rayuwar da ba ta da iyaka. A kan wannan al’amari domin tarbiyyantar da al’umma Manzo (S.A.W) yana cewa: “Ku ziyarci kaburbura domin zasu tuna muku ranar karshe”[1].

Sannan a wani wurin daban yana cewa: “Ku ziyarci makabarta domin kuwa akwai darasi gareku a cikin yin hakan”.[2]

Sannan akwai wasu daga cikin mawakan zamani kamar Marigayi Sayyid Sadik Sarmad yayin ziyarar Kasar Misra da kuma ziyarar Kaburburan fir’aunoni, sai ya yi wata a kan haka wadda take fassara hadisin manzo (S.A.W) game da hakan

## Ziyartar Kaburburan Masoya

Mutanen da suka rasa wani masoyinsu sakamakon alaka ta jini da soyayyar da take tsakaninsu ba zasu taba mantawa da shi ba, zaka ga kodayaushe suna yin tarurruka domin tunawa da shi sannan suna yin kokari wajen girmama shi.

Yayin da mutuwa ta kare su daga saduwa ta jiki, sai suka koma bangare guda; wato suna saduwa da shi ta hanyar ruhi, don haka ne zaka ga suna zuwa wurin da aka rufe shi ta hanyar daidaiku da cikin jama'a domin su ziyarce shi sannan suna yin tarurruka domin tunawa da shi din.

Taron mutuwa da ziyartar kaburburan wadanda suka rasu wata al'ada ce wadda ta hade ko'ina a cikin al'ummar duniya, ta haka ne zamu iya cewa wannan al'amari yana da alaka da halittar mutum. Sakamkon soyayyar da take tsakanin mutane da danginsu wadda take janyo su da su zo domin su ziyarce su yayin da suke da rai, wannan shi yake janyo su ziyarci kaburburansu yayin da ba su da rai; musamman kamar yadda yake a musulunci cewa ruhin mutum sabanin jikinsa ba ya lalacewa.

Ba ma haka ba kawai; bayan haka yakan kara samun karfi na musamman a wannan duniyar sannan yana jin dadin kulawar da masoya suke yi masa ta hanyar ziyartarsa da yi masa addu'a kamar karanta masa fatiha da makamantanta, ta yadda suke kara masa nishadi da karfi.

Don haka bai dace ba mu sha kan mutanen a kan gudanar da irin wannan al'ada wadda take wani nau'in halittar mutum ce, Abin da ya kamata shi ne mu nuna musu yadda ya kamata su aiwatar da hakan, ta yadda sakamakon soyayya ga masoyansu ba zai kai su zuwa ga sabon ubangiji ba.

## Ziyarar Kaburburan Malamai

Abin muka yi Magana a kan shi a sama ya shafi ziyarar sauran mutane ne da suke da alaka ta jini da take tsakanin mamaci da mai ziyararsa. Ta yadda sakamakon wannan ziyara zai biya bukatun wanda ya ziyarta ta hanyar kulawar da ya yi masa, ta yadda masu ziyara zasu tsaftace kabarinsa har ma su sanya wa kabarin turare da sauransu.

Amma a cikin wadannan masoya akwai wadanda suke malamai ne da wadanda suka kawo gyara a cikin duniya wadanda suke da wani matsayi na musamman wanda ya sha bamban da wadanda suka gabata. Wadannan sun kasance tamkar kamar kyandir ne wanda ya kone kansa domin ya haskaka wa waninsa. Haka su ma suka haskaka wa mabiyansu ta yadda suka yi rayuwa a cikin kunci, amma suka bai wa mabiyansu taskar ilimi madawwamiya, sakamakon haka ne suka cancanci yabo da girmamawa.

Musamman malamai wadanda suka koyar da al'umma littafin Allah da Sunnar manzo (S.A.W) ta yadda suka bai wa al'umma abin da zai kai su zuwa ga cin nasarar rayuwar duniya da lahira kuma madawwamiya. Don haka halartar kabarin irin wadannan malaman yana nufin girmama wadanda suke cikin kabarin ne, Sannan kuma sakamakon abin suka yi na yada ilimi ne ya janyo soyuwar al'umma zuwa gare su ta yadda suka yi hidima da kare wadannan ayyuka na su (Littattafai da makamantansu kamar kaburburansu): Hakika duk al'ummar da suke girmama ilimi da malamai ba zasu taba shiga cikin tarkon kuncin ilimi ba.

## Ziyarar Kaburburan Shahidai

Haka nan ziyartar kaburburan Shahidai wadanda suka bayar da jininsu domin kare al'ummarsu da addinin Allah shi ma yana da matsayi na musamman wanda ya fi na sauran mutanen da ba su ba.

Ziyartar kaburburan shahidai wadanda suka rasa rayukansu a kan tafarkin ubangiji, bayan tasirin da yake ga ruhin mutum, sannan yana nuna rikon alkawari a kan tafarkin da suka bayar da jininsu a kai. Wato mai ziyara kamar yana cewa ne yana nan kan tafarkinsu sannan zai yi kariya a kan wannan abin mai tsarki da suka bayar da jininsu. Domin mu kara fahimtar abin da kyau bari mu ba da wani misali wanda yake raye a halin yanzu:

Mutumin da ya ziyarci Dakin Allah, kafin ya yi dawafi yakan yi wa Hajrul Aswad sallama kuma ya sanya hannu ya shafe shi da ma'anar cewa yana yin bai'a ne ga Annabi Ibrahim (A.S) gwarzon tauhidi, da nufin cewa tauhidi shi ne abu na gaba a wajensa. Ta yadda zai yi iya kokarinsa wajen yada shi, amma tunda yanzu ba zai iya kai hannunsa ba zuwa ga Annabi Ibrahim ta yadda zai yi masa bai'a wajen daukar alkari domin wannan aiki shi ne sai ya kai hannunsa ga abin da shi Annabi Ibrahim (A.S) ya bari ta yadda zai gabatar da bai'arsa ta hanyar wannan abin da ya bari. Ya zo a cikin hadisi cewa yayin da mutum yake mika hannunsa zuwa ga Hajrul Aswad yana cewa ne: "Na mika amana da alwakarin da na dauka, sannan na jaddada bai'ata ka sheda a kan hakan".[3]

Ziyartar shahidan Badar da Uhud da Karbala da sauran masoyan da suka bayar da jininsu a tafarkin Allah yana bayyanar da wannan al'amari. Masu ziyarar wadannan wurare masu tsarki sukan yi wa masu wannan wuri sallama da mika gaisuwa zuwa ga ruhinsu tsarkaka, sannan suna daukar alkawari ne a kan cigaba da hanyarsu.

Da wani kalamin muna iya cewa ziyarar kabarin wani nau'i ne na girmama su. Sakamakon an kashe shahidi a kan wani abu mai tsarki da yake girmamawa, duk wanda ya ziyarci shahidi ya girmama shi, a hakikanin gaskiya ya girmama wannan akidar ne wadda a kanta ne aka kashe shi, sannan yana daukar kansa wanda yake biyayya akan wannan hanya.

## Ziyarar Kabarin Manzo (S.A.W)

Ziyarar Kabrin Manzo mai girma (S.A.W) ko kuma wasiyyinsa mai tsarki (A.S) yana da matsayin hukuncin yi musu bai’a ne bayan nuna girmama su a kan abin da suka yi na sadaukar da rayukan su wajen shiryar da al’umma zuwa ga hanyar Allah da yake nunawa. Imami na takwas wato wasiyyin Annabi kuma halifansa da ya yi wasiyya da shi imam Ridha (A.S) a cikin maganganunsa dangane da ziyarar kaburburan ma’asumai (A.S) yana cewa: Kowane Imami yana da alkawari tsakaninsa da mabiyansa ziyarar kabarin Imamai daya daga cikin wannan alkawarin ne”.[4]

A hakikanin gaskiya yayin da mutum yake ziyartar kabarin manzo (S.A.W) ko na Imamai kamar yana yin bai’a da alkawari da su ne cewa ba zai taba bin wata hanya ba a cikin rayuwarsa sai hanyar da suka bari.

Ga abin da mai ziyar kabarin manzo yake cewa: Idan Muhajirun da Ansar wadanda suka halarci yakin Hudaibiyya sun yi maka bai‘a a kan kariya ga addini (Fathi: 18).

Sannan idan matan Makka sun yi maka bai’a a kan gujewa daga yin shirka da sabon Allah (Mumtahna: 12).

Idan har Muminai masu sabo sun samu umarni a kan cewa su zo wajenka domin ka nema musu gafara, ni ma ya manzon Allah ya mai ceton al’umma sakamakon halartata zuwa haraminka da sallama zuwa ga kabarinka ina mai yi maka bai’a a kan cewa zan yi kariya ga addininka sannan in yi nesa daga shirka da sabon Allah, sannan sakamakon haka ina rokonka ka nema mini gafara a wurin Allah.

A nan dole mu fahimci cewa ziyarar kaburburan bayin Allah ya sha bamban da yawon shakatawa domin kuwa yana da manufarsa da ta sha bamban da yawon bude ido. Masu yawon bude ido suna zuwa wuri ne domin su more wa idanunsu, suna neman wurare masu kyau ko na tarihi domin su gane wa idanunsu. Saboda haka gurinsu shi ne: shakatawa da hutawa, duk da cewa idan wannan bai kasance tare da sabon Allah ba, to musulunci ba ya hani da wannan. Amma masu ziyarar kaburburan bayin Allah suna yi ne domin kara samun alaka da masoyinsu da kuma jaddada alkawarinsu da shi, don haka duk wata wahala da zasu hadu da ita wajen isa zuwa gare shi koda kuwa zai kai ga su rika gudu a cikin daji da kafafunsu ne da taka kayoyi suna iya jure wa duk hakan.

Dan yawon bude ido yana neman abin da zai biya bukatunsa na kasantuwarsa mai rai ne shi, amma mai ziyara yana kokarin ya shayar da ruhinsa ta hanyar saduwa da masoyinsa, domin kuwa ba zai iya isa zuwa ga masoyinsa ba, sai ya mika hannunsa zuwa ga kabarinsa wanda yake dauke da kanshi da launinsa.

Tarihi yana nuna cewa: Bayan wafatin manzon Allah (S.A.W) wani bakauye ya shigo garin Madina sai ya zauna a gefen kabarin manzo sai ya karanta wannan aya wadda take cewa: “Da wadanda suka zalunci kansu sun zo a gareka suka nemi gafarar Allah Sannan manzo ya nema musu gafara da sun sami Allah mai karbar tuba mai rahama”.

Sai wannan bakauyen balarabe ya ce: Ya kai manzon Allah gani na zo a wannan wuri domin ka nema mini gafara ina mai neman cetonka zuwa ga Allah”. A lokacin yana cikin kuka sai ya karanta wannan baiti na waka inda yake cewa:

Ya mafificin mutumin da aka bisne jikinsa a wadannan kasashe

Kanshinsa ya bice tudu da kwari na wannan yanki

Ina gabatar da kyautar raina zuwa ga wannan kasa wadda ta boye fiyayyen haliitta[5]

Bayan ya gama wannan baiti na waka sai ya nemi gafara ya tashi ya tafi abinsa.

Wannan balarabe da muka ambata ya fahimci ma'anar ziyarar kabarin manzo daga cikin zuciyarsa tsarkakka, saboda haka ne ya taso ya zo domin ya ziyarci shugaban halitta. Wannan ita ce hikimar ziyartar kaburburan 'yan'uwa, masoya, malamai, shahidai a tafarkin Allah, da shugabannin addini wanda hankali da shari'a suke tabbatar da ingancinsa.

A nan dole ne mu yi bincike ta mahanga daban-daban a kan ziyarar kabari kamar haka:

1-Ziyarar kabarin muminai a mahangar Kur'ani da Sunna

2-Mata da ziyarar kabari

3-Ziyarar kabarin manzo a mahangar manyan malaman musulunci

4-Ziyarar kabarin manzo a mahangar Kur'ani da Sunna

A nan gaba zamu yi bahasi ne a kan wadannan abubuwa guda hudu da muka ambata a sama:

## Ziyarar Kabarin Muminai A Mahangar Kur'ani Da Sunna

Ziyarar kabarin muminai musamman wadanda suke da alaka ta jini da mutum, wani abu ne wanda duk mutanen duniya sun hadu akan yin hakan domin kuwa ya dace da halitta mutum, sannan muna iya fahimtar haka daga wannan aya: "Kada ka sallaci kabarin wanda ya mutu daga cikinsu har abada, Sannan kada ka tsaya a kan kabarinsa domin kuwa lallai sun kafirce wa Allah da manzonsa, Sannan sun mutu alhalin suna fasikai". [6]

Wannan aya mai girama tana ba wa manzo umarnin abubuwa guda biyu kamar haka:

1-Kada ya yi salla ga wadanda suka mutu daga cikinsu da cewa: Har abada kada ka sallaci daya daga cikinsu idan ya mutu.

2-Kada ya je a kabarinsu, domin yi musu addu'a ko makamancin haka: Kada ka tsaya akan kabarinsa.

Bangare na biyu na wannan aya yana da muhimmanci na musamman a gare mu, wannan kuwa shi ne, shin tsayuwa a kan kabari yana nufin yayin rufewa ne ko kuwa yana da ma'ana fiye da hakan? Amma masu tafsiri suna karfafa ma'ana ta biyu ne, wanda zamu yi bayani dangane da abin da suke cewa kan hakan. Bidhawi yana cewa: Ma'anarsa kada ka tsaya a kan kabarinsu yayin rufewa ko ziyara.[7]

Shi ma Suyudi a cikin tafsirul jalalaini[8] ya tafi a kan wannan ra'ayi, Sannan Arif Bursi a cikin tafsirin Ruhul Bayan[9] da Alusi Bagadadi a cikin ruhul ma'ani[10] ya kawo wannan.

Saboda haka Allah madaukaki yana hani ga manzo a kan ya tsaya a kan kabarin munafukai yayin rufewa ne ko kuwa domin ziyara. Wannan yana nuni ne a kan cewa manzo ya kasance yana halartar kabarin muminai yayin rufewa ko kuwa lokacin ziyara, sannan yana yi musu addu'a. Domin kuwa idan ba haka ba, babu ma'ana a yi masa hani a kan wannan al'amari. Saboda haka idan haka ne ma'anar wannan jumla zata kasance kamar haka: Har abada kada ka tsaya a kan kabarin Munafukai.

Sakamakon haka ne zai zamana munafukai sun rasa wannan falala su kuwa muminai suna rabauta daga wannan falala, domin kuwa manzo yana iya halartar kabarin muminai lokacin rufe su ne ko kuwa lokacin ziyara domin ya yi musu addu'a.

## Ziyarar Kabari A Cikin Sunnnar Manzo

Bayan ruwayoyi guda biyu da muka kawo farkon wannan bahasi wadanda suke nuna hikimar ziyara, dole a nan mu kara fadakarwa a kan cewa, manzo da kansa ya kasance yana zuwa makabartar "Bakiyya" domin ziyartar kaburburan musulmi. Sannan tarihi ya tabbatar da hakan kamar haka:

1-Musulim a cikin sahih dinsa yana cewa: An ruwaito daga A'isha cewa duk karshen dare yakan tafi makabarta domin ziyara, duk lokacin da ya shiga wannan wuri yana ce musu: "Amincin Allah ya tabbata gareku ya gidan mutane muminai kun samu abin da ake alkwari da zuwansa a gaba, Kuna rayuwa tsakanin mutuwa da tashin kiyama, mu ma zamu hadu daku, Ya Allah ka gafarta wa wadanda suke a cikin" Bakiyya".

2-Muslim a cikin Sahih dinsa ya ruwaito daga A'isha tana cewa Manzo ya ce mata: Jibril ya sauka zuwa gareshi ya ce masa Allah yana ba da umarni da cewa ku tafi ziyarar mutanen "Bakiyya" Sannan ku nema musu gafara.

A'isha tana cewa: Sai na tambayi manzo cewa, yaya za yi musu addu'a? Sai manzo ya ce ki ce: "Amincin Allah ya tabbata a gareku yaku mutanen wannan gida daga muminai da musulmai, Allah ya jikan wadanda suka riga mu da wadanda zasu zo bayanmu daga cikinsu, Mu ma insha Allah muna nan zuwa mu hadu da ku". [11]

3- Muslim yana ruwaitowa daga Buraida cewa: Manzo (S.A.W). ya kasance yana koyar da Sahabbansa cewa yayin ziyara ga abin da zasu ce: "Amincin Allah ya tabbata a gare ku ya ku mutanen wannan gida muminai muna nan zamu hadu da ku, Muna rokon Allah da ya ba mu lafiya tare da ku.[12]

## Mata Da Ziyarar Kabari

Mata suna da hukunci guda ne da maza dangane da ziyarar masoyansu da waliyyan Allah, domin kuwa hukuncin maza da mata a cikin musulunci duka abu guda ne, sai kawai wurin da aka bambanta maza da mata a wasu wurare na musamman tare da dalili.

Manzo (S.A.W) Yana kira zuwa ga musulmi da cewa: “Ku ziyarci kaburbura domin suna tuna muku lahira”.

Sanan a wani hadisi daban yana cewa: “Ku ziyarci makabarta domin akwai darasi a cikin yin hakan”.

Gaskiya ne wadannan kira tare da lura da yadda aka amfani lamirin maza kamar ya nuna cewa da maza ake, amma kamar yadda muka tunatar cewa kusan dukkan kira da ake yi a cikin Kur’ani da hadisi kamar ana kira ne zuwa ga maza, saboda haka dukkan ayoyin da aka yi amfani da su wajen umartar mutane a kan yin salla da azumi da wannan sigar ne wato an yi amfani da lamirin maza ne, amma wannan umarni ya kunshi mata kamar yadda ya kunshi maza. Kamar yadda yake cewa: Ku tsayar da salla ku bayar da zakka duk abin da kuka gabatar domin kawunanku na alheri to zaku same shi a wajen Allah”[13].

Wannan umarni bisa lura ga ka’idar larabci kamar yana fuskantar maza ne, amma wannan hukunci ya kunshi duka maza da mata ne.

Saboda haka kiran da a aka yi a cikin dukkan wadannan hadisai guda biyu da cewa "ku ziyarci kaburbura” duk da cewa ya fuskantar maza ne amma sakamakon haka ya hada maza da mata ne.

Bayan wannan hadisi kuma a kawai wasu ruwayoyi da suke nuni da halascin ziyarar kabari ga mace, saboda haka a nan zamu ambaci wadannann hadisai kamar haka:

1-Muslim yana ruwatowa a cikin sahih dinsa daga manzo cewa: Jibril ya sauko zuwa gare ni ya ce da ni: Ubangijinka yana ba da umarni da a ziyarci kaburburan mutanen “Bakiyya” Sannan ka nema musu gafara a wajen Allah”.

Sai manzo ya tashi daga bisa shimfidarsa ya tafi Bakiyya domin ziyara, sai A’isha ta bi manzo (S.A.W) daga baya, sai ta fahimci umarnin da Allah ya aiko wa manzo.

A lokacin sai ta tambayi manzo cewa: to yaya zan ziyarci mutanen baki? Sai manzo ya ce: “Ki ce amincin Allah ya tabbata ga nutanen wannan gida daga musulmai da muminai, Allah ya gafarta wa wadanda suka riga mu da wadanda zasu zo bayammu. [14] Wurin da ake kafa dalili a nan shi ne wajen koyar da A’isha yadda ake ziyara, saboda haka idan ya zamana bai halitta ba mace ta ziyarci makabarta, a nan babu ma’ana manzo ya koyar da matarsa.

Sannan bugu da kari A’isha ta kasance tana gaya wa sauran mata dangane da abin da ya auku, saboda haka da wannan zamu iya gane cewa ya hada kowa da kowa cewa ziyarar baki daya ta halatta ga mace da namiji. Domin kuwa matar manzo da sauran mata duk daya suke a wajen hukuncin Allah!

2-Fadima (A.S) ‘yar manzo (S.A.W), kuma daya daga cikin mutanen mayafi (wadanda aka saukar da aya ta 33 suratul ahzab a kansu) Bayan wafatin manzo ta kasance tana ziyartar kabarin amminta wato shahidin Uhud inda take yin salla raka’a biyu sannan ta yi kuka a kabarinsa.

Hakim Nishaburi bayan ya ruwaito wannan ruwaya yana cewa: wadanda suka ruwaito wannan ruwaya dukkansu amintattu ne kuma adalai, ta wannan fuskar ba su da bambanci da maruwaitan Bukahri da Muslim [15].

3-Tirmizi ya ruwaito daga Abdullahi Bn Abi Malika yana cewa: Lokacin da Abdurrahman bn Abibakar ya rasu a wani wuri da ake kira da (Hubsha) Sai aka dauki jana'izarsa zuwa Makka aka rufe shi a can. Bayan wani lokaci sai A'isha wadda take 'yar uwa ce a gare shi ta zo Makka domin ziyarar kabarin Abdurrahaman dan'uwanta, Sannan ta yi wasu wakoki guda biyu wadanda suke nuna tsananin damuwarta a kan rashinsa.[16]

4-Bukhari yana rubuta cewa: Wata rana Mnazo ya ga wata mata gefen wani kabari tana kuka, sai ya ce mata "Ki mallaki kanki sannan ki yi hakuri a kan rasa wani naki da kika yi".[17]

Amma bukhari bai ruwaito cigaban wannan hadisi ba, amma Abu Da'ud a cikin sunan dinsa ya cigaba da wannan hadisi ga abin yake kawowa: Wannan mata ba ta gane manzo ba, sai ta kalubalanci manzo ta ce: Me ya dame ka dangane da abin da musibar da ta same ni? A wannan lokaci sai wata mata da take gefenta ta ce mata kin gane kuwa wannan kowane ne?, Manzon Allah ne (S.A.W).

A wannan lokaci wannan matar domin ta gyara abin da ta yi wa manzo sai ta tafi gidan manzo ta ce masa: Ya manzon Allah ka yi hakuri ban gane kai ne ba. Sa manzo ya amsa mata da cewa: Hakuri a cikin musibar da ta samu mutum shi ne abin da ya dace.[18]

Idan da ziyartar kabarin 'yan uwa ya kasan ce wani aiki ne da ya haramta, maimakon manzo ya yi umarni da yin hakuri, zai ce da ita ne: Ke wannan aiki naki ya haramata a fili. Amma sai ya umurce ta da yin hakuri a kan abin da ya same ta ba wai ta nisanci kabarin ba.

## Amsar wasu tambayoyi guda biyu

Wasu sun haramta ziyarar mata zuwa kaburbura, suna kafa hujjarsu ne kuwa da wadannan hadisai guda biyu kamar haka:

1-“Allah ya la’anci mata masu ziyarar kabari”.

Amsa:

Wannan Hadisi ya rasa sharuddan da ya kamata ya kasance yana da su kafin a iya kafa hujja da shi. Domin bisa ga dogara da dalilai da aka ambata a baya dole ne mu dauka wannan hadisi an shafe shi, Sannan cikin sa’a wasu daga cikin malaman hadisi na Sunna sun dauki wannan hadisi matsayin shafaffe. Tirmiz maruwaicin wannan hadisi yana cewa: Wannan hadisi an shafe shi domin yana nuna lokacin kafin halasta ziyartar kabari ne, amma lokacin da manzo ya halasta ziyarar kaburbura wannan hukunci ya hade mace da namiji babu bambanci.

Kurdabi yana cewa: Wannan hadisi yana Magana ne a kan matan da suke bada dukkan lokacinsu a makabarta ne, ta yadda sakamakon haka ba su bayar da hakkokin mazansu da ya hau kansu. Kuma sheda a kan haka shi ne manzo ya yi amfani da kalmar “Zuwwar” wadda take da ma’anar kambamawa, wato wadanda suke yi yawaita ziyara.

2-Ibn maja yana ruwaito daga Ali bn Abi Dalib cewa: Manzo (S.A.W). Ya fito sai ya ga wasu mata a zaune, sai ya tambaue su me ya sa suke zaune? sai suka ce: Muna jiran jana’iza ne.

Sai ya ce zaku yi wa jana’izar wanka ne?

Suka ce: A’a.

Sai ya ce: zaku dauki gawar ne?

Suka ce: A’a.

Ya ce: zaku saka gawar kabari ne?

Suka ce: A’a.

Sai manzo ya ce: ku koma gida kuma su masu sabo ne ba masu neman lada ba.

Amsa:

Wannan hadisi ta fuskar ma’ana da isnadi ba a bin dogaro ba ne da za a iya kafa hujja da shi, saboda sanadin wannan hadisi (maruwaita hadisin) akwai Dinar bn Amru ya shiga a cikinsu, ta fuskar masu ilimin ruwaya suna cewa ba a san shi ba, kuma mutum ne mai karya mai sabo kuma wanda ake bari. Shin ana iya dogara wajen kafa hujja da irin wannan hadisi wanda maruwaicinsa yake da wadannan siffofi na rauni?

Mu dauka ma dangane wannan hadisi yana da inganci, sam ba shi da alaka da ziyarar kabari, domin kuwa Allah wadai din da manzo ya yi ya shafi matan da suka fito domin kallon janaza, ba tare da wani aiki da zasu yi ba wajen kai jana’zar, saboda haka wannan bai shafi batun ziyarar kaburbura ba.

A nan dole mu yi tunatarwa a kan wani al’amari shi ne, addinin musulunci addini ne wanda ya dace da halitta mutum, kuma mai sauki, manzo yana cewa: “Akidun musulunci akidu ne tabbatattu duk wanda zai shiga cikinsu ya shiga tare da dalilai na hankali”.

Mu dauka cewa mahaifiyar mumini sai ta rasa danta aka kuma rufe shi a karkashin kasa, sai ta damu a kan hakan, abin da kawai zata iya yi a nan shi ne ta ziyarci kabarinsa. A nan idan aka hana ta yin wannan aiki wanda ya

dace da hankali kuma dukkan mutanen duniya sun tafi a kan hakan, wannan zai haifar da muguwar damuwa ga zuciyar uwa. Shin musulunci zai yi hani da irin wannan aiki sannan kuma ya zama addini mai sauki?

Kai asali ma ziyarar kaburbura wani darasi ne kuma mai sanya mutum ya rika tunawa da lahira wanda kuma ya kunshi karanta wa wadanda aka ziyarta fatiha. Ta yaya za a hana mata dangane da samun wannan falala?

Da wani kalamin kasantuwar hikimar ziyarar kaburbura tana kunshe da daukar darasi da tunawa da lahira, ta yaya za a kebance maza kawai ban da mata a ciki?

Kasantuwar ziyarar kaburbura ya nisanta da duk wani sabo, idan muka dauka haka kuma sai aka hana mata a wancan lokaci, to kila sakamakon cewa ba su kiyaye sharuddan da suka kamata ne.

## Ziyarar Kabarin Manzo Mai Girma A Mahangar Malaman Hadisi Da Fikihu

Tare da bibiyar maganganun manyan malaman hadisi da malaman fikihu, zamu ga yadda kodayauhse malaman musulunci suke karfafawa a kan kasantuwar ziyarar kabarin manzo a matsayin mustahbbi mai karfi, Sannan suna kiran mutane zuwa ga ziyarar kabarin manzo mai tsarki.

Takiyyuddin Subki Shafi'i (ya rasu shekara ta 756) Wanda yake daya daga cikin manyan malaman karni na takwas. Yayin da yake kalu balantar akidun Ibn Taimiyya wanda yake inkarin ziyarar kabarin manzo (S.A.W), ya rubuta littafi mai suna (shifa'us sikam fi ziyarati khairil anam) a cikin wannan littafi ya yi kokari ya tattaro ra'ayoyin malaman Ahlus Sunna tun daga karni na hudu har ya zuwa lokacinsa a kan wannan al'amari, a cikin wannan littafi nasa ya yi kokarin tabbatar da nuna cewa ziyarar kabarin manzo yana daga cikin abubuwan da aka sallama a cikin fikihu a kan cewa mustahabbi ne. Manyan malaman hadisi da fikhu sun ruwaito hadisai daban-daban a kan kasantuwar ziyar manzo a matsayin mustahabbi, sannan suka ba da fatawa a kan hakan.[19]

Allama Amini wanda yake bincike na wannan zamani kuma mai tsanantawa wajen bincikensa (1320-1390), a cikin babban littafin nan nasa "Algadir" Ya yi kokari wajen cike abin da ya ragu a kan wannan batu na ziyar kabarin manzo, inda ya yi kokari ya zo da ra'ayoyin malamai arbai'n wadanda suka hada da malaman hadisi da na fikhu har ya zuwa malaman zamaninsa. [20]

Wannan marubuci shi ma ya yi kokari ya samo wasu daga fatwoyin da ba su zo ba a cikin wadancan littattafan guda biyu da muka ambata. Ta yadda ya kawo su a cikin wani karamin littafi da ya rubuta a cikin harshen larabci. Kai har da babban mai fatawar Kasar Sa'udiyya wato sheikh Abdul Aziz bn Baz ya ba da fatwa a kan mustahabancin ziyarar kabarin manzo mai girma.[21]

Kawo dukkan maganganun malamai a kan wannan batu ba zai yiwu ba wannan wuri, saboda haka kawai zamu wadatu da kawo wasu daga ciki ne kawai kamar haka:

1-Abu Abdullaji Jujani Shafi'i (ya rasu a shekara ta 403) Bayan ya yi maganganu a kan girmama manzo sai yake cewa: A matsayin tuanatarwa a yau ziyarar manzo shi ne ziyarar kabarinsa mai albarka.[22]

2-Abu Hasan mawardi (ya rasu a shekara ta 450) Yana rubuta cewa: Jaogoran matafiya zuwa aikin hajji bayan an gama aikin hajji sai ya jagoranci twagarsa zuwa madina domin mahajjata su hada ziyara guda biyu, wato ziyarar dakin ka'aba da ziyarar kabarin manzo. Ta haka ne zasu kiyaye martabar manzo suka kuma bayar da hakkinsa na biyayya gare shi. Ziyarar kabarin manzo ba ya daga cikin farillan ayyukan hajji, amma yana daga cikin mustahabban aikin hajji.[23]

3-Gazali ya yi bayani mai fadi dangane da ziyar manzo (S.A.W), Sannan ya yi bayani a kan ladubban ziyarar manzo Yana cewa: Manzo yace: ziyarata yayin da ba ni da rai duk daya ne da ziyarata a lokacin da nake raye. Sannan duk wanda yake da karfin jiki da dukiya amma bai ziyarce ni ba to ya yi mani tozarci.

Gazali yana karawa da cewa: Duk wanda ya yi nufin ziyarar manzo to ya aika masa da gaisuwa a bisa hanya, sannan a lokacin da idonsa ya hangi itatuwa da bangayen madina sai ya ce: Ya Allah wannan shi ne haramin Manzonka ka sanya shi kariya a gareni daga wuta, Sannan ya zama aminci a gare ni daga azabar wuta da munin hisabi.

Sannan Gazali ya yi tunatarwa dangane da ladubban ziyarar Manzo yana rubuta cewa: Wanda ya ziyarci manzo sai wuce a "Bakiyya" don ya ziyarci kabarin Imam Hasan bn Ali (A.S) Sannan ya yi salla a masallacin Fadima (A.S).[24]

4-Alkali Iyadh maliki (ya rasu a shekara ta 544) yana rubuta cewa: Ziyartar manzo wata Sunna ce wadda kowa ya aminta da ita. Sannan ya ruwaito wasu hadisai dangane da ziyarar kabarin Manzo sannan yana karawa da cewa: Maziyarcin kabarin manzo, to ya kamata ya nemi tabaraki da wurin ibadar manzo (Raudha) Minbarinsa, wurin da yake tsayawa, da shika-shikan da manzo yake jingina a wurinsu da kuma wurin da jibra'il yake saukar wa manzo da wahayi. [25]

5-Ibn Hajjaj Muhammad bn Abdali Kirawani Maliki (ya rasu a shekara ta 738) bayan ya yi magana dangane da ziyarar manzanni da ladubbanta da yadda ake yin kamun kafa (tawassuli) da su da neman biyan bukata daga garesu, sai ya tunatar dangane da ziyarar kamar haka:

"Abin da muka fada dangane da wadansu, a kan abin da ya shafi ziyarar shugaban wadanda suka gabata da wadanda zasu zo kuwa da yadda ake yi masa salla dole ne mu fadi abin da ya wuce hakan. Abin da ya dace shi ne mutum tare da kaskantar da kai ya halarci haramin manzo domin kuwa shi mai ceto wanda ba a mayar da cetonsa. Duk wanda ya tunkare shi ba zai koma ba yana mai yanke kauna ba. Sannan duk wanda ya zo haraminsa yana neman taimakonsa da biyan bukatarsa ba zai rasa abin da yake nema ba".

Sannan ya cigaba da cewa: Malamammu (Allah ya gafarta musu) Suna cewa abin ya dace shi ne: wanda ya ziyarci manzo ya rika jin cewa kamar manzo yana raye ne ya ziyarce shi. "[26]

6-Ibn Hajar Haisami Makki Shafi'i (ya rasu shekara ta 973) Ya kasance ya yi riko da dalilin da dukkan malamai suka hadu a kansu wajen kafa hujja a kan kasantuwar mustahabbancin ziyarar manzo. Sannan yana karawa da cewa: Sabawar wani malami guda a kan wandannan dalilai kamar Ibn Taimiyya ba ya cutar da wadannan dalilai da a ka hadu a kan ingancinsu. Domin kuwa malamai da yawa sun bibiyi maganganunsa kuma suna tabbatar da rashin ingancinsu.

Daya daga cikinsu kuwa shi ne Izz bn Jama'a, kamar yadda Ibn Hajar yake cewa: "Ibn Taimiyya mutum ne wanda Allah ya batar da shi, Sannan ya sanya masa tufafin kaskanci". Sannan Sheikh Takiyyuddin Subki wanda dangane da matsayinsa na ilimi kowa ya aminta da shi, littafi na musamman ya rubuta don kalubalantar fatawoyin Ibn Taimiyya.[27]

7-Muhammad bn Abdul wahab yana cewa: Mustahabbi ne ziyayar manzo amma wajibi ne mutum ya yi tafiya zuwa wajen domin ziyara da yin salla a wajen.[28]

8-Abdurrahman Jaziri marubucin littafin nan (Alfikhu Ala Mazahibil Arba'a) Inda ya kawo fatawoyin dukkan malaman mazahaba guda hudu na Sunna, yana cewa: Ziyarar kabarin manzo yana daya daga cikin manyan

mustahabbai, sannan hadisai sun zo a kan hakan, sannan ya cigaba da kawo hadisai guda shida da suka yi bayani a kan ziyarar manzo da ladubbanta. [29]

Sakamakon cewa duk shugabannin fikihu guda hudu ba su yi wani karin bayani ba a kan abin da aka ambata a sama ba, yana nuna cewa duk malaman wannan zamani suma sun tafi a kan hakan.

9-Shekh Abdul Aziz bn Baz yana cewa: Duk wanda ya ziyarci manzo mustahabbi ne ya yi salla raka'a biyu a (raudhar Manzo) Sanna ya yi wa manzo sallama, Sannan mustahabbi ne ya je "Bakiyya" domin ya yi sallama ga shahidan da a ka rufe a wajen.[30]

A nan zamu takaita da wannan abin da muka kawo dangane da wannan al'amari mai son karin bayani dangane da haka, sai ya koma zuwa ga "Risalar da muka rubuta a kan haka a cikin harshen larabci. [31]

## Ziyarar Kabarin Manzo A Mahangar Kur’ani Da Sunna

**A: A Mahangar Kur’ani Maigirma**

Kur’ani mai girma yana bai wa al'ummar musulmi umarni da su je wajen manzo su nemi gafararsa sannan su nemi manzo (S.A.W) don ya nema musu gafarar Allah madaukaki: "Duk lokacin da suka zalunci kawunansu (suka yi zunubi) idan suka zo wajen manzo suka nemi gafara kuma Manzon ya nema musu gafara wajen Allah, lallai Allah mai rahama ne kuma mai karbar tuba. "[32]

A wani wurin ciki Kur’ani Allah madaukaki yana zargin munafukai da cewa duk lokacin da aka neme su da su je wajen ma'aiki don ya nema musu gafara sai su ki: "Idan aka ce musu ko zo manzo ya nema muku gafara, sai su juya fusakunsu (don nuna rashin amincewa) zaka ga suna kin maganarka suna masu nuna girman kai. "[33]

Shehin malamin nan kuma Ahlussunna, Takiyyuddin Subki, Ya yi imani da cewa: Msuslmi a wannan lokacin ma tare da amfani da wannan aya suna iya zuwa wajen manzo su nemi gafararsa kuma Allah ya gafarta musu. Ya kara da cewa duk da yake wannan aya ta shafi lokacin da manzo yake a raye ne, amma neman gafara ta hanyarsa bai kebanta da lokacin da yake a raye ba. Saboda wannan wani matsayi ne wanda aka bai wa manzo (S.A.W) don haka sakamakon rabuwarsa da duniya wannan matsayi ba zai kau ba.

Mai yiwuwa a ce: Wannan abin da ya zo a cikin wannan aya da muka ambata a sama, ya kunshi nuna matsayi da daukaka ta manzo ne kawai, amma aiwatar da wannan ya kebanci lokacin rayuwarsa ne kawai, amma ba lokacin da baya duniya ba, ta yadda alakarmu da shi ta yanke.

Amma wannan magana sam ba abin karba ba ce, domin kuwa dalilan da zamu ambata a nan gaba suna bayyana cewa rasuwar manzo sam ba ta da wani tasiri a kan wannan al'amari, don haka mutuwa da rayuwarsa babu wani bambanci duk daya ne:

1-Mutuwa ba tana nuna karshen dan Adam ba ne, mutuwa wata sabuwar kofa ce don shiga wata sabuwar rayuwa kuma duniyar da duk abin da yake a ckinta ya fi abin da yake a duniyar da ta gabata ga rayuwar dan Adam, saboda haka mutum rayayye ne a waccan duniya yana gani kuma yana ji. Musamman shahidai wadanda bayan sun dandana shahada zasu cigaba da karbar ci da sha daga Allah madaukaki, kuma suna cikin jin dadi na musamman ta hanyar ruhinsu. Saboda haka zamu yi bayani a kan wannan a nan gaba a cikin bahasin rayuwar barzahu.[34]

2-Ya zo da yawa a cikin ruwaya cewa: Salatin da musulmi suke yi wa manzo akwai mala'iku na musamman masu isar da wannan salati zuwa ga manzo (S.A.W) don haka duk inda mutum yake idan ya yi wa manzo salati zai isa zuwa ga manzon. Kamar yadda yake cewa: "Ku yi mani salati, salatin yana isa zuwa gare ni daga duk inda kuke".[35]

3-Musulmi a wajen tahiyar salla an umurce su da su yi wa manzo sallama, sannan su yi masa gaisuwa, "Assalamu alaika ayyuhan nabiyu warahamatullahi wa barakatuhu" Wannan gaisuwa ba wai kawai an umurci musulmi ba ne da su yi ta zuwa ga manzo amma shi ba ya jin abin da suke yi, Manzo yana raye kuma yana sauraren mu lokacin da muke yi masa salati.

Wadannan abubuwan da muka fada a sama suna nuna cewa Manzo yana raye a rayuwar barzahu, sannan yana da alaka da mu kuma yana jin abin da muke yi. Sannan yana jin rokonmu kuma yana biya mana bukatunmu a lokacin da ya dace. Saboda haka a nan ya kamata mu ce wadannan ayoyi da muka yi bayani a sama, Suna da ma'ana mai fadi, saboda haka yanzu ma suna kiranmu da ziyarar manzo a kabarinsa kuma mu nemi gafara kuma ya nema mana gafara ga Allah, sannan mu nemi bukatunmu daga gareshi. Saboda haka ya zo a cikin ziyarar manzo da ake karantawa a haraminsa cewa mai ziyara ya nemi gafarar Allah ta hanyar manzon tare da kula da ma'anar ayar da muka yi bayani a sama. Saboda haka ziyarar manzo ba wani abu ba ne sai kawai yin salati ga manzo da kuma neman bukatu da gafarar Allah ta hanyar mazon. Saboda haka wadannan ayoyi na sama suna iya zama sheda a kan inganci da mustahabbancin ziyarar manzo (S.A.W).

Wata sheda kuma a kan wannan batu shi ne, bayan rasuwar Manzo wani balarabe ya shigo Madina yana karanta wannan aya da muka ambata, sai ya ce: "Na zo wajenka ina mai neman gafara daga zunubaina kuma ina mai neman ceto gareka zuwa ga Ubangijina".[36]

Sannan muhimmin abu kamar yadda Subki yake cewa: Kiran al'ummar musulmi da su ziyarci manzo kuma su nemi gafara da bukatunsu daga gareshi wata alama ce ta karrama manzo da girmama shi. Kuma tabbas wannan girmamawa ba ta kebanci lokacin rayuwarsa ba, saboda girma da mukamin ruhinsa a wajen Allah wani abu ne wanda ba mai shakku a kansa kuma madawwami ne, saboda haka bai kebanta da wani zamani ba sabanin waninsa.

Saboda haka ne malaman Tafisri suka tafi a kan cewa, girmama manzo bai kebanci lokacin rayuwarsa ba, saboda haka dole ne a kiyaye shi har bayan rasuwarsa. Har ma ayar da ke umurta musulmi da su rika magana a hanakali a gaban manzo, tana nan a matsayinta, inda Allah yake cewa: "Ya ku wadanda kuka yi Imani kada ku daga muryarku saman muryar Annabi[37]".

Saboda haka bai kamata mutum ya rika magana da karfi a cikin haramin mazon mai tsaira ba. Sannan wannan aya an rubuta ta a kan kabarin manzo, wanda duk ya je wannan wuri ya gane wa idonsa hakan.

**B: A Mahangar Sunna**

Mun ga hukunci da matsayin Kur’ani a kan wannan al'amri, yanzu abin da ya rage shi ne ku ga kuma me Sunnar manzo ke cewa a kan hakan..

Ruwayoyi da dama sun zo akan wannan batu na ziyarar kabarin manzo, kuma malamai sun yi kokarin tattara su da kuma tabbatar da danganensu. Saboda haka a nan a matsayin misali zamu kawo wasu daga cikinsu kamar haka:

1-Takiyyuddin subki (ya yi wafati a shekara ta756h) a cikin littafinsa "Shifa'us sikam" ya ruwaito hadisi tare da sanadi ingantacce. [38]

2-Nuruddin Ali bn sahmudi (ya yi wafati 911H) ya ruwaito ruwaya 17 akan wannan batu, a cikin littafinsa na tarihin Madina sannan kuma ya inganta sanadinsa.[39]

3-Muhammad fukki daya daga cikin Malam Azahar tare da shafe sanadi ya ruwaito matanin ruwayoyi 22 a kan ziyarar manzo.[40]

4-Allama Amini tare da tare da bin diddigi wanda ya ci a yaba masa, ya tattara ruwayoyi da dama a kan ziyarar manzo (S.A.W) saboda haka a nan kawai zamu yi nuni da daya daga cikin ruwayoyi da ya samo daga littafi 41 da a ka ruwaito a kan hakan. Al-Gadir

Saboda haka kawo dukkan ruwayoyin da danganensu ba zai yiwu ba a nan, saboda haka kawai a nan zamu takaita ne da kawo wasu kawai daga cikinsu. Wadanda suke son karin bayani sai su koma zuwa littafin da aka ambata a sama.

Hadisi na farko: "Wanda duk ya ziyarci kabarina aljanna ta wajaba a gareshi"[41]. wannan hadisi Allama Amini ya ruwaito shi tare da sanadi daga littafi 41.

Hadisi na biyu: Dabarani a cikin mu'ujamul Kabir, Gazali a cikin ihya'u ulum daga Abdullahi bn umar, Manzo yana cewa: "Duk wanda yazo ziyara kuma saboda kawai ziyarata ya zo, to ya wajaba in cece shi a ranar kiyama. "

Hadisi na uku: Darul Kutni ya ruwaito daga Abdullahi bn umar cewa manzo (S.A.W) ya ce: Duk wanda ya ziyarce ni bayan wafatina a lokacin aikn hajji, to kamar ya ziyarce ni a lokacin da nake a raye. "

Hadisi na hudu: Darul kutni ya ruwaito daga bn Umar cewa manzo (S.A.W) ya ce: "Duk wanda ya ziyarci kabarina kamar ya ziyarce ni a lokacin da nake a raye. " A nan ya kamata mu yi nazarin matsayin ziyara a wajen Imaman Ahlul-bait (A.S)

## Ziyar Manzo A Ruwayar Ahlul-Bait (A.S)

1-Imam Bakir (A.S) yana cewa Manzo (S.A.W) yana cewa: "Duk wanda ya ziyarce ni ina raye ko bayan na yi wafati zan kasance mai cetonsa a ranar kiyama"[42]

2-Imam Ali (A.S) yana cewa: "Ku cika hajjinku da manzon Allah a lokacin da kuka fito daga dakin Allah, domin kin ziyartarsa rashin girmamawa ne gare shi, an umurce ku da yin hakan, tare da ziyarar kaburburan da aka umurce ku zaku karashe hajjinku."

3-Imam Sadik (A.S) daga manzon tsira (S.A.W) yana cewa: "Duk wanda ya zo Makka don aikin hajji amma bai ziyarce ni ba, zan banzatar da shi a ranar tashin kiyama, wanda kuwa ya ziyarce ni cetona ya wajaba a garesa, duk wanda cetona ya wajaba a garesa, aljanna ta wajaba a garesa. Saduk: Ilalish shara'i'i

4-Imam Sadik (A.S) yana cewa Manzo. (S.A.W) yana cewa: "Duk wanda ya ziyarce ni zan zama mai cetonsa a ranar tashin kiyama". [43]

Ruwayoyin da dukkan bagarori guda biyu suka ruwaito ta fuskar ma'ana ba su da bambanci, saboda haka suna karfafa abubuwa guda biyu kamar haka:

A-Duk wanda ya je Makka bai ziyarci Manzo ba, to ya yi wa manzon jafa'i.

B-Duk wanda ya ziyarci Manzo, Manzo zai cece shi a ranar kiyama. Saboda haka don mu takaita wadannan ruwayoyi guda takwas daga Shi’a da Sunna sun wadatar wanda yake son karin bayani sai ya koma zuwa ga littfan da muka ambata.

## Tattaunawar Imam Malik Tare Da Mansur Dawaniki

Kadhi Iyadh ya nakalto tattaunawar Imam Malik tare da Mansur Dawaniki kamar haka:

Mansur Dawaniki wanda yake khalifa ne mashahuri na Abbasiyya, wata rana ya shiga haramin Manzo yana magana da karfi. Malik a lokacin shi ne Fakih a Madina sai ya juya zuwa ga Mansur ya ce: Ya kai shugaban Muminai, kada ka daga muryarka a cikin wannan masallaci, Allah madaukaki ya koya wa wasu mutane ladabi inda yake cewa: "Kada ku daga muryarku saman muryar Annabi"[44] Sannan ya ya bi wasu gungu daga cikin mutane ya ce: Lallai wadanda suke kasa da muryarsu a gaban manzon Allah, su ne wadanda Allah ya jarabba zukatansu da takawa"[45] Sannan Allah yana cewa Wasu gungun mutane wadanda suke hayaniya a bayan gidan Manzo suna cewa: Ya Muhammad ka yi sauri ka fito daga cikin gida, Allah yana kaico da halinsu, yan cewa: "Lallai wadanda suke kiranka daga bayan gida mafi yawansu ba su da hankali".[46] Sannan ya cigaba da cewa girmama Manzo a lokacin da ba shi da rai kamar lokacin da yake da rai ne babu bambanci.

Lokacin da Mansur ya ji wannan magana sai ya zo da kansa wajen Malik ya ce: A lokacin da nake addu'a zan kalli kibla ne ko kuwa kabarin Manzo?

Sai Malik ya ba shi amsa da cewa: Me ya sa zaka juya wa Manzo baya alhali kuwa shi ne tsaninka kuma tsani ga babanka Adam har zuwa ranar tashin kiyama, don haka ka kalli kabarin Manzo ka nemi ceto daga gare shi Allah ya amshi cetonka. Allah yana cewa: A lokacin da suka zalunci kawunansu suka zo gare ka suna neman gafarar Allah manzon zai nema musu gafara..."[47]

## Ziyarar Kabari Da Kiyaye Asali

A cikin wannan bahasi namu mai tsawo kawai mun yi amfani ne da ruwayoyin da suke nuni a kan wannan al'amari daga ruwayoyin Ahlus Sunna. Amma muna da ruwayoyi da dama daga maruwaitanmu na Shi’a da suka ruwaito daga Imaman Ahlul Bait (A.S). Wadanda ba mu yi nazari a kansu ba. Sdaboda haka idan aka duba littattafan hadisai na Shi’a za a tabbatar da wannan al'amari cewa, ziyarar Manzo da Ahlul Bait (A.S) yana daga cikin abin da yake karbabbe ga kowa a cikin wannan mazahaba ta Ahlul Bait (A.S) sakamakon haka ne aka rubuta littattafai? da dama a kan hakan wadanda a ka fi sani da suna "almazar" wato wurin ziyara, daga cikin wadannan littattafai? kuwa wanda duk ya fi shahara shi ne, "Alkamil Ziyarat" wanda shehin malamin nan mai suna Ja'afar bn muhammad bn kulawaihi ya rubuta. (ya yi wafati 367H).

A nan zamu kara da cewa, kiyaye abubuwan da suke na asali yana daya daga cikin ayyukan addinin musulunci. Abin da muke nufi da asali kuwa shi ne abin da yake bayyanar da gaskiyar musulunci da cigabansa har ya isa zuwa ga dukkan zamuna.

Addinin musulunci addini ne da yake na duniya baki daya, don haka har zuwa tashin kiyama zai kasance matsayin addini cikakke har karshen duniya. Saboda haka dole ne mu yi iya kokarinmu mu ga cewa mun kiyaye asalin wannan addini don ya isa kamar yadda ya zo zuwa ga wadanda zasu zo a nan gaba.

Saboda haka ziyarar kabarin Manzo da Ahlul Bait (A.S) yana daya daga cikin kiyaye asalin addini, don haka barin hakan bayan wani tsawon zamani sai ya zamana an manta da wannan babban aiki mai albarka. Saboda haka dangane da wadanda zasu zo nan gaba sai ya zamana wadannan wurare na musamman na manyan bayin Allah ya koma kamar wani abin tatsuniya.

Kasancewar zuwan Isa (A.S) a yau wani abu ne wanda ba abin shakka ba ga al'ummar musulmi, amma a yammacin duniya musamman ga matasa al'amarin Annabi Isa ya zama kamar wani abin tatsuniya, wannan kuwa ya faru ne sakamakon rashin wani abu wanda yake nuna gaskiyar samuwar shi Annabi Isa (A.S) a hannayen mutane. Wannan kuwa ya faru ne sakamakaon canza littafinsa da a ka yi, don haka dangane da shi kansa Masih da mahaifiyarsa da sauran manyan sahabbansa babu wani abu na hakika wanda yake tabbas daga garesu yake. Don haka sakamakon tsawon zamani a yau al'marin masihiyya ya zamana kimarsa ta rage kuma ya shiga cikin wani halin kokwanto da rashin tabbas. Kamar yadda a yau ziyarar Manzo wadda take daya daga cikin abu na asali a cikin addinin musulunci kuma mai nuna hakikanin matsayi da samuwar Manzo tana neman ta zama wani abu marar muhimmanci a cikin al'ummar musulmi, kuma ya zamana an ajiye ta a gefe guda. Don haka sakamakon tsawon zamani akwai yiwuwar abubuwan asali na addinin musulunci da waliyyan Allah, su shiga cikin wannan hadari mai girma.

Saboda haka al'ummar musulmi dole ne su tashi tsaye domin kare wannan hadari da ya fuskanto su, wannan kuwa yana samuwa ne ta hanyar kiyaye duk wani abu da ya shafi sakon manzanci da Imamanci, ta yadda za a rika tuna shi a kowane zamani. Saboda haka ziyarar wadannan manyan bayin Allah tana daya daga cikin hanyoyin kiyaye su daga bacewa da kuma

yin tunani a kansu a kowane lokaci. Saboda haka sakamakon yin hakan ba za a taba watsi da matsayin wannan muhimmin al'amari ba, ta yadda za iya kulle kofar ganawa ta hanyar ruhi da wadannan manyan bayin Allah ga al'ummar musulmi. Saboda haka da ikon Allah a nan gaba zamu yi magana a kan kiyaye wadannan wurare masu tsarki.

## Tafiya Domin Ziyarar Kabarin Manzo (S.A.W)

Ziyarar Kabarin dukkan musulmi da musamman ziyarar kabarin Manzo wani abu ne wanda yake mustahabbi mai karfi a cikin musulunci. Sannan malaman hadisi daga Sunna da Shi'a sun ruwaito hadisai da dama a kan mustahabbancin ziyarar kabarin Manzo wadanda wasu daga cikinsu sun gabata a cikin bahasin da ya gabata ta yadda babu wani malami daga cikin malaman musuluncin da ya ba kansa damar yin shakku a kan mustahabbancin ziyarar Manzo. Wannan kuwa ya hada har da Muhammad bn Abduh wanda yake da wasu masatlolin dangane da abin da ya shafi annabawa, a nan ba kawai ya yi shiru ba ne, sai dai ya yi magana a kan mustahabbcin ziyarar Manzo (S.A.W). Sannan mun kawo abin da yake cewa dangane da hakan a bahasimmu na baya. Tare da la'akari da kasantuwar mustahabbicn ziyarar Manzo, amma msulmi sun kasu a kan wannan kyauta ta ubangiji:

1-Mazauna Madina

Mazauna Madina sakamakon makwautaka da suke da ita da Manzo (S.A.W). Suna iya ziyartarsa ba tare wata wahala ba don aiwatar da wannan mustahabbi.

2-Mazauna sauran wurare a cikin duniya

Mazauna sauran sassan duniya dole ne su yi tafiya domin su damar yin sallama ga kabarin Manzo Su ce: "Amincin Allah ya tabbata a gareka ya manzon Allah".

A nan tambaya ita ce; menene hukuncin wannan tafiya a shari'a?

Jawabain wannan tambaya kuwa a fili yake domin wannan amsa tana matsayin gabatarwa ce domin aiwatar da aikin mustahabbi, saboda haka a akidar wasu malamai tana matsayin mustahabbi, wasu kuwa suna cewa tana hukuncin halal "Mubah" ne.

Duk yadda ta kama kasantuwar wannan tafiya domin aiwatar da mustahabbanci ce ba zata taba zama haramun ba. Domin kuwa ba zai inganta ba a hankali Allah madaukaki ya umurce mu da aikin mustahabbi na ziyartar Manzo sannan ya haramta abin da yake matsayin gabatarwa ne domin aiwatar da wannan aikin. Saboda haka daga nan muna iya gane cewa hukuncin wannan tafiya domin aiwatar da wannan aiki ta halitta. [48]

Kamar yadda yake a tarihi shi ne musulman da suke rayuwa a sauran sassan duniya wato ba wadanda suke rayuwa ba a garin Madina sukan daure kayansu domin tafiya zuwa ziyarar kabarin Manzo mai girma a nan ga wasu misalai a kan hakan:

Bilal wanda yake mai kiran salla ne na Manzo kuma Manzo ya kasance yana kaunarsa. Bayan tafiyar Manzo ya zabi ya tafi wani wuri yiwa musulunci hidima, sakamakon haka ne ya yi hijara daga garin Madina. Wani dare sai ya ga Manzo a cikin mafarki yana ce masa: Wannan wane irin rashin kulawa ne Bilal? Yanzu lokaci bai yi ba da zaka ziyarce ne?

Lokacin da Bilal ya tashi daga barci yana cikin bakin cikin da ya mamaye masa zuciya, sai kawai ya tanaji abubuwan bukata domin yin tafiya kuma ya tafi zuwa Madina. Lokacin da Bilal ya shiga a cikin Raudar Manzo yana kuka da murya mai karfi a wannan hali ya dinga goga fusakarsa a kan kabarin Manzo (S.A.W). A nan haka sai kwatsam abin kaunar? Manzo wato Hasan da Husain (A.S) sai suka yi wajensa sai ya kama su ya runguma, sai

suka ce masa, Muna tsananin son mu ji muryar kiran sallarka, kiran sallar da kake yi wa kakanmu manzon Allah (S.A.W).

A lokacin sallar Asubahi sai Bilal ya hau wurin da ya kasance yana kiran salla a zamanin Manzo (S.A.W) ya kira salla. A lokacin da kiran sallarsa ya mamaye Madina Ya girgiza garin Madina a wannan lokaci, a lokacin da ya yi kalmar shahada a cikin kiran sallarsa sai duk mutane suka daga murya suna kuka, a lokacin da kuwa ya yi shahada a kan manzancin Manzo (Ashhahadu anna Muhammadar Rasulullah) ai sai duk mutanen Madina suka yi waje suna kuka. Kamar yadda ake rubutawa: Bayan ranar da Manzo ya yi wafati madina ba ta taba ganin irin kukan da ta gani ba a wannan lokaci.[49]

2-Umar bn Abdul Aziz ya kasance yana hayar mutane domin su zo daga Sham zuwa madina domin su yi masa sallama ga Manzo. Subki a cikin Futuhus Sham yana rubuta cewa: Lokacin Umar bn Abdul Aziz ya yi Sulhu da mutanen Kudus sai Ka'abul Akhbar ya shigo wajen kuma ya musulunta, a wannan lokaci Umar ya ji dadi kwarai da musuluntarsa. Sai Umar ya ce masa: Kana iya bi na mu tafi madina mu ziyarci kabarin Manzo ta yadda zamu fa'idantu da ziyararsa? Sai Ka'ab ya amsa wa khalifa abin da ya nema daga gareshi, ya yi shirin tafiya tare da khalifa. A lokacin da Umar ya shiga garin madina, farkon abin da ya fara yi shi ne ya shiga masallacin Manzo ne domin ya yi wa Manzo sallama.[50]

Duk da yake ba mu da bukatar mu kafa sheda a nan da irin wadannan misalai, domin kuwa al'ummar musulmi duk tsawon karnoni? sha hudu sun dauki wannan al'amari na ziyara Manzo a matsayin mustahabbi kuma suna tafiya Madina domin su aiwatar da wannan mustahabbi.

Subki dangane da tafiyar ayari-ayari zuwa ziyarar Manzo ya yi maganganu da dama a kan hakan, ya kara da cewa masu ziyara bayan sun gama aikin hajji sukan kama hanyar Madina ne domin su kai wa Manzo ziyara, ya kara da cewa: wata sa'a sakamakon fahimtar ladar da yake cikin yin hakan sukan dauki hanyar da tafi nisa zuwa Madina, domin su samu lada mai yawa a kan haka. Sannan ya cigaba da cewa, wadanda suke tunanin cewa dalilin da ya sa mutane suke tafiya madina shi ne domin su ziyarci masallacin Manzo kuma su yi salla a ciki wannan kuskure ne, domin kuwa abin masu ziyarar suke fada ya saba wa wannan tunanin. Domin manufarsu a kan wannan ziyara shi ne su ziyarci kabari Manzo, sannan wannan shi ne gurinsu na ziyarar Madina. Domin kuwa idan manufarsu a kan wannan tafiya shi ne ziyartar masallaci, me ya sa ba su tafiya Kudus domin su ziyarci masallacin baitil mukaddas wanda yin salla a cikinsa bai gaza wa yin salla a masallacin Manzo ba?

Kamar yadda yake haduwar malamai a kan wani hukunci yana nuna ingancin wannan hukunci a shari'a haka nan haduwar dukkan musulmi a kan wani aiki yana nuna mafi daukaka kasantuwan wannan abin a cikin shari'a.[51]

## Masu Haramta Tafiya Don Ziyarar Manzo

Har zuwa karshen karni na bakwai malamai sun hadu a kan wannan al’amari cewa tafiya domin aiwatar da wani aiki na mustahabbi koda ba ta zama mustahabbi ba to alal akalla ta halasta. Amma a farkon karni na takwas, Sai Ibn Taimiyya ya yi riko da hadisin Manzo wanda Abu Huraira ya ruwaito ta yadda ya saba wa dukkan malamai da suka hadu a kan wannan al’amari. Wannan ruwaya kuwa da Ibn taimiyya ya yi mafani da ita, an ruwaito ta ne ta fuska guda uku, amma abin da yake iya tabbatar wa Ibn taimiyya da manufarsa ya zo da fuska biyu ne kamar haka:

1- Kada a yi nufin tafiya sai zuwa masallatai guda uku: Wannan masallaci nawa, masallacin ka’aba da Masallacin Kudus.[52]

2- Ana yin tafiya ne kawai zuwa ga masallatai guda uku[53], Ibn taimiyya ya yi riko ne da zahirin wannan hadisi domin tabbatar da manufarsa, ta yadda ya yi da’awar cewa domin aiwatar da ayyukan ibada masallatai uku ne kawai mutum zai iya zuwa domin yin hakan. Saboda haka ziyarar Manzo wanda yake matsayin ibada ba ya daya daga cikin wadannan abubuwa guda uku. Wannan kafa hujja ta Ibn Taimiyya kuwa idan muka lura da kyau zamu iya gane rashin ingancinsa, domin kuwa ba shi da kafafu masu karfi.

Domin kuwa mun san cewa jumlar da take kebewa tana ginuwa daga sassa guda biyu kamar haka:

1-Jumlar da ake kebewa daga gareta: "Ba wanda ya zo wurina".

2- Jumlar da a ka kebance "Sai Ali"

Hadisin da ya gabata ya ginu ne ta hanyar jumloli biyu ne:

1-jumla ta farko jumlar da aka kebance daga gare ta "Kada ku yi tafiya. "

2-Jumla ta biyu kuwa, wadda aka kebance: "Sai masallatai uku".

A jumlar ta farko abin da aka kebance bai fito ba a fili, bisa la’akari da ka’idar larabci a nan dole mu kaddara wata jumla, wadda zata iya zama daya daga cikin wadannan jumloli guda biyu kamar haka:

1-Mai yiwuwa ka iya cewa "masallaci" ne. (wato kada ka yi tafiya zuwa kowane masallaci sai masallatai guda uku)

2-Mai yiwuwa ana nufin "wuri" ne (kada ka yi tafiya zuwa wani wuri sai masallatai guda uku) Saboda haka bisa ga tsammani na farko, zai zama ma’anar jumla zai zama haka, wato kada ka yi tafiya zuwa kowane masallaci sai masallatai guda uku da aka ambata.

Saboda haka idan muka dauki wannan ma’ana zai zama cewa Manzo yana magana ne a kan masallatai, wato don mutum ya yi salla kada ya yi wahala don tafiya kowane masallaci sai masallatai guda uku da aka ambata. Saboda haka a nan ziyarar Manzo ba ta cikin abin da aka hana a cikin wannan hadisi domin ba a kansa ake Magana ba. Sannan dalilin da ya sa aka yi hani tafiya wani masallaci domin yin salla domin sauran masallatai hukunci guda garesu babu wani wanda ya fi wani daraja daga cikinsu, saboda haka yayin da mutum yake da damar yin salla a daya daga cikin masallatai me zai sanya ya sha wahala domin ya tafi waninsa.

Misali kamar idan akwai masallacin jumma’a a wani gari me zai sanya mutum ya tafi wani gari domin ya yi sallar jumma’a a can, domin kuwa ladar da zai samu a wancan masallacin ba ta dara wadda zai samu ba a wannan na garinsu.

Amma dangane da wadancan masallatai uku abin ba haka yake ba, domin salla a cikin daya daga cikinsu ya fi salla a cikin sauran masallatai, saboda haka tare da kula da cewa a cikin wannan hadisi an yi magana ne kawai a kana masallatai, don haka tafiya zuwa wasu wurare bai shafi wannan hani na hadisi ba, saboda haka ba ya magana a kan halasci ko haramcin yin hakan.

Amma idan muka dauki ma’ana ta biyu ma’anar wannan hadisi zata kasance kamar haka: kada ka yi tafiya sai zuwa wurare guda uku (masallatai guda uku da muka ambata).

Idan muka dauki wannan ma’ana dogaron Ibn Taimiyya yana iya zama dai-dai. Amma tare da lura da yadda tarihin musulmai ya tafi a kan mustahabbacin tafiya zuwa kabarin Manzo (S.A.W), domin ziyara tana nuna mana rashin ingancin wannan hadisi.

Na farko kamar yadda muka gani a cikin hadisin da ya gabata, ana iya tsammanin wata ma’ana daban, sakamakon wannan ma’ana kuwa ba za a samu wani fito na fito ba a hadisai da ayoyi da kuma tarihin musulmi da suke nuni a kan halascin ziyarar Manzo. Kuma tare da daukar ma’anar farko musamman kasantuwar mu dauki cewa kalmar da zamu iya kaddarawa ita ce masallaci, domin kasantuwar dacewarta da abin da ya zo a cikin jumlar, kuma shi ne abin da ya fi dacewa ya kuma fi karfi. Saboda haka wannan hukunci wanda Ibn Taimiyya ya dauka zai zama sam ba shi da ma’ana a nan.

Haka nan idan muka dauki ma’ana ta biyu wato muka dauka cewa ai a nan ana nufin "wuri" wato bai halitta ba mutum ya tafi wani wuri sai wadannan wurare guda uku, wannann kuwa zai bayar da ma’anar da ba ta dace ba, sannan fitowar wannan kalma daga mai hikima musamman Manzo ba zai yiwu ba. Wato ya zama an hana zuwa kowane wuri sai wadannan wurare guda uku (Masallacin ka’aba, Kudus da Masallacin Manzo). alhalin musulunci ya halatta wasu tafiye-tafiye da dama a cikin musulunci wasu daga cikinsu ma mustahabbi ne. Misali kamar tafiya domin neman ilimi, ko tafiya domin kasuwanci ko tafiya don sada zumunci, tafiya don yawon bude ido, tafiya domin jihadi da dai sauran tafiye-tafiye da suke halas wadansu ma mustahabbi a musulunci.

Saboda haka a nan dole ne mu dauki ma’ana ta farko wato masallaci, cewa kada mutum ya yi tafiya domin ya je wani masallaci sai masallatai guda uku, domin kuwa su ne su kafi sauran masallatai matsayi. Da wannan ne zamu fitar da batun tafiya domin ziyarar Manzo domin ba ita ake magana ba a cikin wannan hadisi.

Bayan dangane da ingancin wannan hadisi koda an dauki ma’ana ta farko, akwai shakku a cikinsa. Domin kuwa yana nufin wannan magana ta fito daga bakin Manzo inda take nuni da cewa tafiya zuwa kowane masallaci ba ta inganta sai masallatai guda uku. Alhali kuwa ruwayoyi sun zo a kan cewa Manzo (S.A.W). Wasu ranakun Asabar yakan tafi kasa, wata sa’a bisa abin hawa domin ya je masallacin "Kuba?" domin ya yi salla raka’a biyu a wajen. Wannan masallaci a zamanin da Manzo yake a raye yana da tazarar kilo mita 12 tsakaninsa da Madina.[54]

## Ziyarar Masallatai Guda Bakwai

A sassa daban-daban na garin Madina akwai wasu masallatai guda bakwai wadanda mahajjata sukan ziyarta yayin da suka je Madina, Idan ma muka kara da (masallacin Raddi shams, da na Bilal da na Ijaba) Yawansu zai wuce bakwai. Mahajjata suka yi salla raka'a biyu a wadannan masallatai musamman sukan fi ba da muhimmanci a kan masallacin Imam Ali (A.S) Yanzu tambaya zata iya zuwa cewa: Idan har yin salla a wadannan masallatai ba shi da wani fifiko a kan sauran masallatai, to me ya sa mahajjata suke zuwa ziyarar wadannan masallatai sannan su yi salla a cikinsu? alhali kuwa wannan bai zo ba a cikin shari'a, saboda haka wannan zai zama "Bidi'a" kenan a cikin addini.

Amsar wannan tambaya kuwa a fili take:

Tafiya domin ziyarar wadannan msallatai ba wai don yazo a cikin shari'a ba ne, ko kuma yin salla a cikin wadannan masallatai yana da wani fifiko na musamman, sam ba haka ba ne manufar tafiya zuwa wadannan wurare sai daya daga cikin biyu ne kamar haka:

1-Tunawa da musulman farko wadanda suka kasance cikin mawuyacin halin yakin Khandak amma a cikin wannan hali ne suka gina wadannan masallatai don su yi salla kuma suka cigaba da yakinsu. Domin kuwa wasu daga cikin wadannan masallatai suna wuraren da aka gwabza tsakanin sojojin tauhidi da na shirka yayin da aka kashe gwarzon shirka (Amru bn Abdu wud) kuma sakmakon haka ne gwamnatin dagutu ta kawo karshe.

Halartar musulmi a wadannan wurare tana tuna musu da wadannan abubuwa da suka faru a wannan wuri, sannan yana kara karfafa alakarsu da wadancan musulman farko.

2-Amma ma'ana ta biyu kuwa da zata iya zama dalilin da ya sa musulmai suke zuwa wadannan masallatai ita ce, domin neman tabarraki daga wadannan wurare, domin jinanan shahidai a kan hanyar tauhidi a wadannan wurare ne ya zube, Saboda haka wannan wurare sun sheda kai da kawon shahidan musulunci, sannan kuma wuri na kai-da-kawon manyan musulmai.

Wadannan manufofi su ne suke sanya musulmi suna tafiya zuwa wadannan wurare da makamantansu, kamar wurin da aka yi yakin khaibar da Fadak, duk sun samo asali ne daga wadannan manufofi guda biyu.

Amma yin salla a wadannan wurare bayan musulmi sun shiga wadannan masallatai domin aiwatar da umarnin ubangiji cewa duk yayin da mutum ya shiga wani masallaci to ya gabatar da salla raka'a biyu a matsayin gaisuwa ga shi masallacin. Saboda haka ba wannan ba ne hadafinsu na zuwa wadannan masallatai ba domin su gabatar da salla a wajen. Wannan niyya tana zuwa ne bayan sun shiga masallatan.

## Girmama Kaburbura Masu Tsarki

Al'ummun da suke raye a kasashen da suka cigaba a duniya zaka ga suna kokari wajen kare kayan tarihi kuma suna nuna soyayyarsu ga wadannan abubuwa na tarihi. Sannan suna iya kokarinsu da su kare wadannan kayan tarihi don kada su bata ko su lalace. Domin kiyaye wadannan kayan tarihi kuwa wadanda suke nuna cigabn su a tsawon tarihi har ma'aikatu na musamman suka samar da ma'aikata kwararru domin kawai wannan aiki. Sakamakon haka ne ba su ba da wata dama da zata sanya wani guntun abu daga cikin wadannan kayan tarihi da suka hada da wani allo wanda aka yi wani rubutu a kai ko guntun jirgin ruwa da ya bata. Domin sun yi imani da cewa wadannan kayan tarihi suna ba da wata sheda ce ta musamman ta su wadannan al'umma. Mutanen da suka yanke daga al'ummarsu da manyan tarihinsu da suka gabata suna da hukuncin yaro ne wanda ya bata daga hannun iyayensa. Cigaban musulunci wani cigaba ne wanda yake mai girman gaske wanda a karnonin tsakiya shi ne kawai cigaban da babu kamarsa.

Sakamakon koyarwar da Musulmai suka samu daga littafinsu na sama, sun kafa cigaban da ba a taba yinsa ba a tarihi. Wanda ya kai kololuwarsa a cikin karni na hudu, ta yadda gabas da yammacin duniya suka shaida haka, kamar yadda ya gina Tajmahal na kasar Indiya da Kasar (Spain) sauran gine-gine masu ban al'ajabi, wanda ta hanyar kaitsaye ko kuma ba kaitsaye ba. Kamar yadda masana na yamacin duniya suka tabbatar da cewa cigaban yammacin duniya ya samu asali ne ta hanyar Andulus ko kuma ta hanyar yakin da ya auku tsakanin musulmi da kiristocin yammacin duniya.

Cigaban musulunci ya fara ne da aiko manzon Musulunci (S.A.W) ko kuma da wata ma'ana ya fara ne da haihuwar shi manzon, Sannan da taimakon mabiyansa ya cigaba ta kafuwa da yaduwa a sauran sassan duniya. Gine-ginen da suke dangane da Manzo ko kuwa wasu daga cikin sahabbansa suna daga cikin wannan cigaba na musulunci. Sannan kuma wannan ba mallakin wani ba ne ta yadda zai yi abin da ya ga dama da su, wannan na dukkan al'ummar musulmi ne. Saboda haka babu wata hukuma ko wasu mutane da zasu yi abin da suka dama da wannan kayan tarihi da cigaban musulunci ba tare da izinin sauran musulmi ba. Ta yadda ta hanyar yaki da bidi'a da tsayar da tauhidi su kawar da wadannan kayan tarihi.

Tarihin musulunci yana gaya mana cewa: An haifi manzon musulunci ne a shekara ta 570 bayan haihuwar Annabi Isa (A.S) Sannan bayan ya kai shekara 40 da haihuwa aka aiko shi a manzanci. Bayan aiko shi da manzanci ya yi shekara 13 a garin Makka yana isar da wannan sako. Bayan wannan ne tare da umarnin ubangiji ya bar inda aka haife shi zuwa garin Madina, Inda a can ne ya yi shekara 10 yana isar da wannan sako na musulunci kuma ya yi fito na fito da mushrikai makiya musulunci, sakamkon bayar da shahidai da ya yi a wannan hanyar ya samu damar daga tutar musulunci a dukkan yankin kasashen Makka da kewayenta (yanki mai girma daga cikin Jaziratul Arab) A shekara ta 11 bayan hijara ne ya koma zuwa ga rahamar Ubangijinsa. Sannan bayan wafatinsa Sahabbansa suka cigaba da wannan aiki na yada musulunci a sassan duniya daban-daban.

Wannan kuwa ya shafi rayuwar da kokarin Manzo da iyalansa da da mabiyansa ne (kamar yadda muka fadi cewa shi ne tushen wannan cigaba) Saboda haka dole mu yi kokari wajen kare wannan asali.

## Kaburburan Shugabannin Addinin Musulunci Suna Nuna Tarihin Musulunci

Dole ne mu kula da cewa duk wani abu da zai faru a wani zamani yana kore duk wani shakku ga wadanda suke rayuwa a wannan zamani. Amma tare da gushewar zamani sakamkon ko-in-kula na mutane zai sanya wannan yakini da tabbas da yake ga mutane ya ragu. Ta yadda a hankali zai zama ana shakku da tararrabi a kan faruwar wannan abin, ta yadda wani lokaci ma zai koma kamar wata tatsunniya. Abubuwan da suka faru ga addinan da suka gabata a lokacin da suka faru babu wani shakku ko taraddudi a kan faruwarsu, amma sakamakon rashin kulawa a yau sun zama kamar tatsunniya.

Maimaita wannan mummunan al'amari dangane da musulunci yana da matsala fiye da yadda ya faru a sauran addinan da suka gabata. Domin kuwa addinin musulunci addini ne wanda har zuwa ranar tashin kiyama dukkan mutane dole ne su yi biyya a gare shi, ta yadda zasu sadu da haske ta hanyar hakan. Mutanen da zasu zo nan gaba kuwa zasu iya biyayya ga wannan addini yayin da suka kasance sun samu yakini dangane da hakikaninsa.

Babu shakka daya daga cikin hanyar kiyaye wannan tabbaci na hakikanin addinin musulunci kuwa shi ne kiyaye abubuwan da suka shafi rayuwar Manzo da sauran shugabannin addinan musulunci.

Magabatanmu Allah ya rahamshe su, sun yi hidima mai yawa dangane da al'ummar yanzu, ta yadda suka kiyaye mana abubuwan da suka zo tun farkon zuwan musulunci. Sakamakon haka ne kai tsaye muke kiran sauran al'umma zuwa ga wannan addini wanda yake hakikaninsa bai samu wani canji ba, ta yadda muke cewa: Karni goma sha hudu ne da suka gabata shugaban Bani Hashim ya ta shi da manzanci daga Allah ya kuma kira mutane zuwa ga Tauhidi da kaurace wa bautar gumaka da kafirci, bayan Mu'ujizozin da ya zo da su. Sannan ya zo da littafi mai girma wanda ya karya makiyansa da shi. Sannan har zuwa yanzu wannan Mu'ujizata har abada tana nan ba tare da wani canji ba.

Wanda kafin ya fara bayyana kiransa ya kasance yana tafiya kogon hira domin yin ibada ga Allah madaukaki. Bayan cika shekara arba'in da rayuwarsa ya fara kiransa. Wasu mtane daga cikin mutanen Makka suka yi imani da shi, yayin da wasu mafi yawa suka kaurace masa, har ma suka yi nufin su hallaka shi, amma Allah da ikonsa ya boye shi a wani kogo da ake kira (Thaur) wanda yake kudancin garin Makka, ta yadda ya tsira da makiya. Bayan nan kuma ya yi hijira zuwa garin Madina, a wannan gari ne mutane Aus da Khazraj (wadanda ake kira da Ansar) suka amsa kiransa suka taimake shi. Manzo a tsawon zamansa a garin Madina ya gwabza yaki mai tsanani tsakaninsa da mushrikai da Yahudawa, Ta wannan hanyar ne ya gabatar da shahidai da dama a tafarkin Allah ta yadda suka ba da jinansu a yakin Uhud, Khaibar da Hunain. Manzo (S.A.W). Ta hanyar aika mabiyansa zuwa sassa daban-daban na wannan nahiya ta kasashen larabawa ya samu damar isar da sakonsa zuwa ko'ina a wannan lokaci. A shekara ta 11 ne bayan hijira ya koma zuwa ga ubangijinsa kuma ya yi umarni da rufe shi a cikin dakinsa. Bayan wafatinsa mabiyansa suka cigaba da hanyar da ya bari, ta yadda ba tare da bata lokaci ba, ya yada wannan addini tare da al'adun da Kur'ani ya zo da su a dukkan sassan duniya.

Wannan shi ne wani yanki na tarihimmu wanda bayan wucewar karni 14 ake maimaita shi. Saboda haka dole mu yi kokarin wajen kare wannan tarihi na mu da duk abin da ya shafi hakan, ba wai ta hanyar wasu dalilai ba marasa tushe mu ruguza wannan tarihi namu!.

Kamar yadda ya kasance mu shagala game da kiyaye wadannan kayan tarihi, ta yadda babu bambanci a wurin dangane da samuwarsa da rashinsa duk daya yake, (abin da ma ya fi muni shi ne yadda ake ganin cewa rusa wadannan abubuwa yaki ne da yaduwar shirka) Ta yadda a cikin kankanin lokaci an manta da wasu abubuwa na tarihin musulunci, don ha ka bayan wani lokaci zai yiwu a fara shakku dangane da wasu abubuwa na hakikanin wannan kira da Manzo ya zo da shi. Ta yadda kamar su Salman Rushudi maimakon canza addini sai ya yi kokarin inkarin addinin da tarihinsa baki daya.

## Daukar Darasi Daga Tarihi

Mutum kodayaushe yana kokari ne ya kalli kowane al’amari ta hanyar idanu ko makamancinsu, domin kuwa ilimin da yake samuwa ta wannan hanya mutum ya fi dogara a kansa. Cikinsa a babban hanyar da ake bi domin tabbatar da wani abu dangane da abin da ya shafi rayuwar zamantakewa, kuma wanda aka fi dogara da shi domin yana ba da sakamakon da ake samun yakini, shi ne tarihi, Kur’ani mai girma yana ba da tarihin magabata ne domin daukar darasi. [55] Dangane da shari’un da suka zo daga sama muna iya daukar shari’ar Annabi Isa (A.S) a matsayin misali. A akidar musulmi Annabi Isa matsayin annabin Allah yake, wanda yake mai albishiri ne ga zuwan Manzo Muhammad (S.A.W), sannan ya zo da littafi mai suna "Injil" wanda yake dauke da haske a cikinsa, amma muna samun tabbas a hakan ne ta hanyar Kur’ani mai girma.

Amma sakamakon matashin da yake yammacin duniya ba shi da imani da Kur’ani ta yadda zai kalli Annabi Isa ta wannan fuskar, a yau dangane da zuwan Annabi Isa da littafinsa yana da shakku a kansu. Domin kuwa ba shi da wata alama ta wannan kira a hannunsa ta yadda zata taimaka masa ya samu yakini a kan hakan. Domin kuwa Masih ba shi da kabari ko mahaifiyarsa da sahabbansa da zasu tabbatar da zuwansa. Sannan littafinsa an hakaito shi ta hanyoyi daban-daban ta yadda zai yi wahala mutum ya gane gaskiyar al’amarin. A takaice babu wani abu wanda zai tabbatar wa matashin yammacin duniya gaskiyar zuwan Annabi Isa da littafinsa. Saboda haka sabanin magabatansa yana shakku a kan hakikanin wannan al’amari.

Saboda haka mu musulmi dole mu dauki darasi daga wannan abin da yake faruwa daga kiristanci. Ta yadda zamu kiyaye duk wani abu wanda yake ya zo daga Manzo kuma yana matsayin sheda ne ga da’awar da shi Manzo ya zo da ita, (duk yadda ya kasance abu dan karami ne) Ta yadda zamu kare duk wani abu wanda zai sanya wadanda zasu zo bayammu su yi shakku a kan gaskiyar addinin musulunci, kamar yadda matashin yammacin duniya yake shakkun gaskiyar Annabi Isa da Injila.

Muna iya amfana daga ayoyin Kur’ani da suke nuni da cewa: Al’ummun da suka gabata sun kasance suna kiyaye duk wani abin da manzonsu ya zo da shi, ta yadda suke tafiya da shi yayin wani kwami mai zafi da yake a gabansu. Ta yadda ta hanyar neman albarkaci da wannan abin daga annabawansu don neman samu cin nasara daga mushrikai abokan gabarsu. A matsayin misali Bani Isra’il sun kasance suna tsaron wani akwati wanda duk abin da musa da iyalansa suka bari yana cikinsa, sannan suna neman tabarruki daga gare shi kuma yayin karo da makiya suna daukar shi domin neman cin nasara.[56]

Kasantuwar albarkar da muhimmancin wannan akwati ya zamana mala’iku suke daukarsa. Idan har ya kasance kiyaye wasu abubuwa na magabata (kamar wannan akwatin) wani abu ne marar kyau, to me ya sa Kur’ani mai girma yake ambaton wannan al’amari da harshe na yabo, kuma me ya sa mala’iku suke daukarsa, sannan me ya sa bayan dauke wannan akwati daga "Amalika" a cikin wannan aya ya zama wata alama ce da take nuna wanda zai jagoranci wannan runduna ta yaki?! Yara wadanda ba su balaga ba, su ne suke wasa da kayan da iyayensu suka bar musu, ta yadda cikin sauki suna iya batar da su. Amma magadan da suke da hankali kuma

sukan amfani da matsayin wannan abin da iyayensu suka bar musu, suna rike wadannnan kaya ne iya karfinsu. Al'ummar musulmi ma sakamakon cigaban da suka samu bayan wafatin Manzo (S.A.W), su kiyaye duk wani abu da ya bari, wannan kuwa har da kwarar gashinsa sun kasance sun sanya ta wani wuri na musamman suka ajiye ta.

## Matsayin Gidajen Annabawa A Cikin Kur’ani

Gidajen annabawa da manyan bayin Allah suna da wani matsayi na musamman, wannan kuwa a fili yake matsayin da suke da shi bai shafi wani abu na duniya ba ne, domin idan da haka ne, gidajensu ba su da wani bambanci da sauran gidajen mutane domin an gina su ne da yumbu da tubali kamar na kowa. Wadannan gidaje suna da wannan matsayi ne sakamakon mutane masu matsayi da suka zauna a cikinsu.

Kur’ani mai girma[57] yana siffanta hasken ubangiji da fitila mai haske ta yadda yake haske kamar tauraruwa. A ayar da take biye ma wannan aya kuwa ya nuna cewa wurin wannan haske yana gidajen wasu mutane masu girma wadanda suke ambaton Allah a ciki safiya da yamma.[58]

A cikin wannan aya jimlar da take cewa "Ana tasbihinsa safiya da yamma, tana nuna dalilin da ya sa aka daukaka wadannan gidajen wadanda aka ambata a cikin ayar da ta gabata. A ayar da take biye mata kuwa an siffanta masu yin ibada a cikin wadannan gidaje ne, inda yake cewa: "mutane ne wadanda kasuwanci ba ya shagaltar da su daga ambaton Allah da tsayar da salla, domin suna jin tsoron ranar da zukata da idanu suke jujjuyawa suna tsorata.[59]

Wannan aya tana bayani ne a kan girma da daukakar gidajen da ake zikirin Allah ake kuma tsarkake shi a cikinsu. A nan dole ne mu yi bayani a kan abubuwa guda biyu kamar haka:

1-Me ake nufi da gidaje a cikin wannan aya?

Masu tafsiri sun yi sabani a kan ma’anar wannan ayar ta yadda kowane ya dauki daya daga cikin ma’anonin kansa:

A-Ana nufin gidaje a cikin wannan aya da masallatai guda hudu

B-Ana nufin dukkan masallatai ne a cikin wannan aya

C-Ana nufin gidajen Manzo ne

D-Masallatai da gidajen Manzo

A cikinwadannan ma’anoni da aka ambata a kasa ma’ana ta uku ce kawai zata iya dai-dai kamar yadda zamu kawo dalilai da suke karfafa hakan.

1-Ta fuskar lugga kalmar Buyut jam’i ne na bait wato gidan kwana. Ibn manzur ya tafi a kan cewa bait yana nufin gidan mutum. Ragib kuwa yana cewa bait shi ne inda mutum yake fakewa da dare. Amma mawallafin "almunjid kuwa cewa ya yi, ma’anar bait tana nufin wurin zama wanda ya hada da hema da gidan da aka gina kasa da tubali.

Saboda haka fassara kalmar bait da masallaci wanda yake wurin ibada na kowa da kowa bai inganta ba, domin kuwa ba wurin da mutum yake fake wa ba ne da daddare. Saboda haka idan ma har ya inganta, amma abin zai zo ga kwakwalwar mutum shi ne gidan kwana, don haka idan har yana nufin masallaci ne ana bukatar abin zai nuna hakan. Ba tare da hakan ba, ba za a karbi wannan ma’ana ba.

Da wani kalamin ma Bait ya samu asali ne daga baituta wato mutum ya tsaya wani wuri har zuwa safe. Idan har ana mabata gidan mutum da bait saboda mutum yana kwana a cikin wannan gida ne har zuwa safe. Tare da kula da wannan ma’ana ta kalamar bait, fassara ta da ma’anar masallaci yana bukatar abin da yake nuna hakan, ba tare da wannan ba ba za a karbi wannan fassara ba.

2-Kur’ani duk lokacin da zai yi magana a kan wurin da al’umma suke bauta yana amfani ne da kalmar "masjid" ko "Masajid" ne. Sakamakon haka ne wannan kalma an yi amfani da ita sau 28 acikin Kur’ani mai girma. Amma duk lokacin da za a yi nagana a kan wurin da mutane suke kwana a kan yi amfani da kalmar "Maskan, Ma’awa" ne. Sannan an yi amfani da kalmar bait ta fuskar jam’i ko tilo. Saboda haka wannan kalma ta zo sau 66 a cikin Kur’ani da wannan manufa, sakamakon haka muna iya fahimata cewa a cikin Kur’ani kalmar "Masjid" da "bait" ba suna nufin ma’ana guda ba ne. saboda haka idan aka nemi fassara su da ma’ana guda zai zama da’awa ba tare da dalili ba.

Idan Kur’ani ya kira masallacin Ka’aba da "baitullahi"[60] ba don yana wurin bautar Allah ba ne, domin kuwa mun san cewa Ka’aba alkibla ce ta masu bautar Allah ba wurin da ake ibada ba. Saboda haka hada sunan Allah da wannan wurin kawai yana nuna girmamawa ne, kai ka ce wannan gida na Allah ta yadda za a girmama shi girmamawa ta musamman.

3-Akwai muhimmin bambanci tsakanin masallaci da gida, Bait ana nufin bangaye guda hudu da aka yi wa rufi, amma masjid kawai bangaye guda hudu ne, wato rufi ba sharadi ba ne kafin ya zama masallaci. Da yawan akan gina masallatai a wuraren da suke da zafi ba tare da rufi ba, wanda daya daga cikinsu shi ne masallacin ka’aba, alhalin kuwa gidan da mutum yake kwana yana bukatar rufi.

Wannan aya da zata zo a kasa tana bayar da sheda a kan bukatar gida daga rufi:

"Ba don hikimar Allah ta yi rigaye ba akan cewa komai zai kasance bai daya, da mun sanya gidajen wadanda suka kafirce wa Ubangiji mai rahama masu rufi da azurfa da tsanin da suke amfani zuwa sama".[61]

Wannan aya tana bayyana cewa "bait" sabanin "Masjid" yana da rufi, sannan ba don wata maslaha ba da Allah madaukaki ya bambanta gidajen kafirai da na muminai ta yadda zai sanya gidajen Kafirai rufinsu ya zama na azurfa, amma sai bai yi hakan ba.

4-Jalaluddin Suyudi ya ruwaito daga Anas bn Malik Yana cewa: Yayin wannan aya wadda take cewa "A cikin gidajen da Allah ya yi Umarni da a daukaka….". Sai ya karanta a cikin masallaci, sai wani daga cikin sahabban Manzo ya mike ya tambayi Manzo me ake nufi da wadannan gidaje?

Sai Manzo ya amsa masa da cewa: Ana nufin gidajen Annabawa, a wannan lokaci sai Abubakar ya mike ya ce: Ya nuna gidan Ali da Fatima (A.S) ya ce wadannan gidajen suna cikin wadanda Allah ya yi izini da daukaka su?. Sai Manzo (S.A.W). ya amsa masa da cewa: E, suna ma daga cikin mafi daukakarsu.[62]

Imam Bakir (A.S) yana cewa: Abin da ake nufi da gidaje a cikin wannan aya shi ne, gidajen Annabawa da gidan Ali (A.S)[63]

Bisa dogaro da wadannan dalilai muna iya fahimtar cewa abin da ake nufi da gidaje a cikin wannan aya ta cikin Suratun Nur shi ne gidajen annabawa da waliyyan Allah, sakamakon tasbihi da tsarkake Allah da ake yi a cikinsu yake da wani matsayi na musamman, kuma Allah ya yi izini da yin kokari wajen a daukaka su.

5-Sannan dalili wanda yake a fili a kan cewa abin da ake nufi da gidaje a cikin wannan aya su ne, ayoyi guda biyu da suka zo kamar haka: Allah madaukaki yana yi wa Annnabi Ibrahim da matarsa magana kamar haka:

A-"Rahmar Allah da albarkarsa ta tabbata a gare ku ya ku ma'abota gida[64];

B-Allah Kawai ya yi nufi ya tafiyar muku da kazanta yaku Ahlul Bait, ya kuma tsarkake ku tsarkakewa[65]; Kai ka ce wadannan gidaje su ne cibiyar hasken ubangiji.

Tare da kula da wadannan dalilai guda biyar da muka kawo muna iya cewa: Masati da daukakar wadannan gidaje sakamakon wadanda suke zaune a cikinsu ne, suna tasbihin ubangiji suna tsarkake shi. A hakikanin gaskiya wannan aya tana magana ne dangane da gidaje irin gidajen Annabi Ibrahim da Manzo (S.A.W). Wannan kuwa sakamakon tasbihi da tsarkake ubangiji da ake yi a cikinsu. Shi ne ya sanya Allah madaukaki ya daga martaba da darajarsu.

Mai yiwuwa a ce: Karkashin wannan aya ana cewa: "Yana tasbihinsa a cikinsu safiya da yamma": wato abin da ake nufi da "Buyut" Masallatai, domin kuwa musulmin farkon zuwan musulunci sun kasance suna halarta sallar jam'i baki dayansu. saboda haka tasbihi da tsarkake ubangiji ana yin sa ne a cikin masallaci.

Amma wannan fahimta ba daidai ba ce, domin kuwa ana aiwatar da sallar wajibi ne kawai a cikin masallatai, sannan mustahabbi ne a gabatar da sauran sallolin mustahabbi a cikin gidaje. Sannan ya kamata ma mutum ya kasa ibadarsa zuwa gida biyu, wato wani bangare na farilla ya aiwatar da su a cikin masallaci, sannan bangaren nafiloli ya gabatar da su a cikin gida.

Mai yiwuwa wasu suga wannan bai inganta ba, amma hakikanin al'amarin haka yake domin kuwa ruwayoyi da dama sun karfafa hakan. Muslim a cikin sahih dinsa, ya kawo babi mai zaman kansa wanda yake nuna mustahabbancin sallar nafila a cikin gida. A kan haka ya ruwaito ruwayoyi da dama, amma a nan kawai zamu kawo wasu a matsayin misali:

Manzo mai tsira da aminci yana cewa: "Fiyayyar sallar mutum a cikin gidansa, sai dai sallolin wajibi"[66].

Wannan ruwaya tana nuna mana cewa Manzo (S.A.W) da sauran sahabbansa suna yin sallolinsu na nafila a cikin gidajensu, sakamakon haka ne gidajen annabawa da na salihan bayi suka zama wurin zikirin Allah da tsarkake shi. Sannan kuma dalilin wannan ne Allah ya ba da izini a kan daukaka su.

A yanzu dole ne mu ga me ake nufi daga matsayin wadannan gidaje! me ake nufi da daukaka wadannan gidaje?

A baya mun yi bayanin cewa, kafa hujja da wannan aya yana bayyanar da abubuwa guda biyu ne. Abu na farko kuwa shi ne, bayyanar da ma'anar "buyut" wanda muka yi cikakken bayaninsa a baya, yanzu lokaci ya yi da zamu yi bayani a kan abu na biyu wanda shi ne daukaka wadannan gidaje da Allah yake horo da shi.

Hakika kalmar "Rafa'a" cikin Kur'ani tana zuwa ne da ma'anar daga gini kamar yadda ta zo a cikin wannan ayar: "Shin halittar su ita ce tafi wahala ko kuwa sama wadda ya gina ta?! Sannan ya daga rufinta ya kuma daidaita ta?![67]

Amma kalmar "rafa’a" a cikin wannan aya ba yana nufi yin gini ba, domin kuwa an dauka cewa akwai gida ne, Kur’ani yana magana a kan siffofin wannan gida ne. saboda haka abin da ake nufi da wannan kalma a cikin wannan aya shi ne daga matsayinsu da girmama su, mafi yawan masu tafisiri sun dauki wannan ma’ana duk da cewa wasu daga ciki sun tafi a kan ma’anar da muka ambata a baya. [68]

A bayyane zamu iya cewa: Wuraren da Allah yake ambatar "Buyut" yana nufin gidajen da bayin Allah suke kwana suna yin tasbihin ubangiji kuma suna tsarkake shi. Saboda haka daukaka wadannan gidaje ba ya nufin daga gininsu ko rufinsu ba ne, abin da ake nufi shi ne daga matsayi da martabarsu. Daya daga cikin wannan girmamawa da daga matsayinsu kuwa shi ne ya zamana an tsarkake su daga dukkan wata kazanta, sannan duk inda suka dan lalace a gyara su.

Dukkan wannan aiki za a yi shi ne saboda girmama wadanda suka kasance a cikin wadannan gidaje suna tasbihin ubangiji suna salloli kuma ba su kin fitar da zakka, domin girmama wadannan mutane ne Allah ya yi horo da a girmama wadannan gidaje, sannan a kare su daga rushewa.

Kowa ya san cewa an rufe Manzo (S.A.W) a cikin gidansa, wato a wurin da ya kasance yana ambaton Allah da yabonsa. Saboda haka tare da bin hukuncin wannan aya gidan Manzo ya cancanci girmamawa da daukaka matsayinsa, sannan a kiyaye shi daga kowane irin rushewa da lalacewa. Sannan kuma a kaurace wa sanya masa duk wani nau’i na kazanta, kai da yawa daga bangarorin Madina kaburburan manyan bayin Allah ne. Kamar yadda ya zo a cikin ingantattun ruwayoyi sayyida Fadima (A.S) ita an rufe ta ne a cikin gidanta[69]

Haka nan Imam Hadi da Imam Askari (A.S) an rufe su a gidajensu wadanda suka kasance suna ibada da zikirin ubangiji a cikinsu. saboda haka wadannan gidaje bisa la’akari da wannan aya sun cancanci a daukaka su, sannan dole ne a kauce wa rusa su domin ya saba wa wannan aya. A unguwar Bani Hashim a garin Madina shekaru kadan da suka gabata gidan Imam Hasan da Husain (A.S) da makarantar Imam Sadik (A.S) sun kasance a wadannan wurare, Marubucin wannan littafi shi kansa ya ziyarci wadannan wurare, amma abin bakin ciki tare da fakewa da fadada masallacin Manzo duk an rusa wadannan wurare masu dimbin tarihi da albarka. Duk da cewa ana iya yin wannan aiki na fadada masallacin Manzo (S.A.W) ba tare da rusa wadannan wurare ba.

## Soyayyar Manzo (S.A.W) Da Iyalansa

Ayoyi da hadisai da dama sun zo domin bayani a kan soyayya ga Manzo da ‘yan gidansa (A.S). Kur’ani ya nuna mana cewa imanin abin ceta shi ne ya kasance yana tare da wanda yake son Manzo da jihadi a tafarkin Allah fiye da komai a cikin zuciyarsa: "Ka ce idan iyayenku da ‘ya’yanku da matanku da ‘yan’uwanku da dukiyoyinku wadda kuka tara, da kasuwanci da kuke tsoran ku fadi a cikinsa, da gidajenku da kuke kaunarsu, idan sun kasance sun fi soyuwa a gareku daga Allah da manzonsa da jihadi a tafarkin Allah sai ku saurara har al’amarin Allah ya zo, Allah ba ya shiryar da mutane fasikai".[70]

Ayar sama tana magana ne a kan abubuwa guda uku wadanda mafi yawa soyayyar mutum takan ta’allaka da su, wato Iyalai da dukiya da gidaje da saye da sayarwa. Amma mumini na hakika shi ne wanda Allah da mazonsa da jihadi a tafarkin Allah ya fi soyuwa a gare shi fiye da wadancan abubuwa da aka ambata. Amma a wata aya ana bayani ne a kan soyayyar iyalan gidan Manzo ga abin da take cewa: "Ka ce ban nemi wani abu a kan sakon manzancin da na zo da shi ba a matsayin lada sai soyayya ga iyalan gidana".[71]

Sannan Manzo yana bayyana wasu abubuwa guda uku wadanda suke nuna dandana zakin imanin mutum, daya daga cikinsu shi ne soyayya ga Allah da shi manzon: Abubuwa guda uku ne duk wanda yake da su to ya dandana zakin imani, daya daga cikinsu kuwa shi ne ya kasance a wajan mutum son Allah da manzonsa ya fi komai a wajensa… Ruwayoyi da suka zo dangane da son Manzo da iyalansa sun wuce gaban mu kawo su a cikin wannan littafi, saboda haka a nan zamu takaia da wasu ruwayoyi a matsayin misali dangane da wannan al’amari, muhimmin abu a nan shi ne mu san ta yaya wannan soyayya zata tabbata, domin mutum ya isa zuwa ga wannan hadafi akwai hanyoyi guda biyu:

1-Mutum ta hanyar magana da ayyukansa ya yi koyi da koyarwar Allah da manzonsa, ta yadda zai kasance a rayuwa ya yi kokari ya ga bai kauce wa koyarwarsu ba, domin kuwa idan mutum ya zamana yana tsananin soyayya ga wani ba zai taba saba masa ba. Saboda haka ne ake cewa "soyayya ita ce biyayya". Wato sonka da abu yana lizimta maka da yi masa biyayya.

Sannan Imam Sadik (A.S) a wasu baituka yana bayyana bambanci tsakanin soyayya ta gaskiya da nuna soyayya da ba ta hakika ba, Inda yake bayani akan cewa: Kana sabon Allah alhali kana nuna soyayya gare shi, Wannan ba zai taba yiwuwa ba, Domin da sonka ya kasance a gaskinya ne, to da ka yi biyayya a gare shi, Domin kuwa masoyi yana bin abin da abin so yake so. [72]

2-Bayyana soyayya ta hanyoyi daban-daban kamar haka:

A- Nuna farin cikin yayin da masoyi yake cikin farin ciki, da nuna bakin ciki yayin da masoyi yake cikin bakin ciki;

B-Gabatar da buki na farin cikin a lokacin haiwuwar Manzo ko lokacin tayar da shi a matsayin ma’aiki;

C-Yada maganganunsa da abin da ya rubuta;

D-Kiyaye kayan tarihin da suka shafe shi;

D-Girmama Kabarinsa da yin gini domin kiyaye shi daga lalacewa;

Aikata wadannan abubuwa da makamantansu wadanda suke sun halasta a musulunci, yin su ga Manzo da iyalan gidansa ya nuna kauna ne a gare su.

Tirmizi yana ruwaitowa a cikin sunan dinsa: "Manzo (S.A.W) ya kama hannun Hasan da Husain sai ya ce: Duk wanda yake so na ya kuma so wadannan yara guda biyu da babansu da mamansu, to zai kasance a matsayina a ranar kiyama[73].

Kowannenmu ya san da cewa babban jikan Manzo yana rufe ne a "bakiyya" Sannan mai biye masa yana rufe a Karbala, Sannan wadannan wurare kodayaushe suna ganin al'ummar musulmi masu ziyara, Saboda haka duk wani gini kowane abu wanda za a yi domin kiyaye wadannan wurare, nau'i ne na nuna soyayya ga wadannan jikoki na Manzo kuma bin umarnin Manzo ne a kan soyayya gare su, kamar yadda muka yi bayani a ruwayar da ta gabata.

A yau al'ummu da dama suna kokari wajen tunawa da manyan tarihinsu (kamar sojoji da 'yan siyasa da wadanda suka yi wasu ayyuka na gyara) ta hanyoyi daban-daban, sakamakon haka ne suke halarta jana'izarsu yadda ya kamata. Sannan su rufe a wani wuri na musamman a karkashin gini mai kawatarwa, ta yadda wadanda zasu zo a nan gaba kamar yadda na yanzu suke kulawa ta musamman a kan su, suma su yi kulawa da girmamamawa ta musamman a kan wadannan manyan mutane. Don haka mu ma musulmi dole mu yi kokari don yin gine-gine da zasu kare kabuburan manyan mutanemmu.

## Kaburburan Manzanni Da Tarihin Magabata Ma’abota Tauhidi

Tafiye-tafiye domin bude ido zuwa wuraren da aka rufe annabawa da ‘ya’yansu wani abu ne wanda yake ba sabo ba a cikin al’umma. Wannan kuwa yana nuna cewa mabiya annabawa suna nuna kulawa ta musamman dangane da wadannan wurare, tare da gina gine-gine a kan kaburburansu suna kare su daga rushewa. A yanzu a kasashen Iraki, Palasdin, Jordan, Misra da Iran, akwai kaburburan annabawa (A.S) wadannan aka yi gine-gine masu kawatarwa ta yadda kodayaushe mutane suna zuwa wurin domin ziyara. Sannan dakarun musulunci da su kai hare-hare don bude garuruwan Sham, sam ba ruwansu da wadannan kabuburan annabawa, ba ma haka ba kawai sun bar mutanen da suke hidima a wadannan wurare don su cigaba da aikinsu a wajen kamar yadda suke a da. Sannan ba su nuna rashin amincewarsu a kan hakan ba ko kankani. Idan da yin gine-gine a kan kaburburan annabawa wani aiki ne da ya haramta kuma ya shafi shirka, da wadannan dakaru da suka zo da umarnin khalifa domin bude wadannan garuruwa duka sun rusa wadannan gine-gine, amma koda wani dan karamin canji ba su yi ba ga wadannan kaburbura an cigaba da tafiyar da su kamar yadda suke kafin wannan lokaci. Sannan har zuwa yanzu wadannan gine-gine suna nan kamar yadda suke ta suke jawo hankalin al’ummar musulmi da ma duk mai bin addinan da Allah ya aiko da su. Sannan a farkon zuwan musulunci ma musulmai sun rufe annabinsu a cikin dakinsa, kuma babu wani daga cikin wadannan musulmai da yake tunani cewa yin gini a kan kabarin Manzo haramun ne.

Sannan binciken littattafan tarihi da labaran tafiye-tafiyen masana addinin muslunci yana bayar da shedar cewa akwai daruruwan kaburbura a kasar da wahayi ya sauka da sauran kasashen musulmi:

1-Mas’udi wanda ya rasu 345Bh. wanda yake shahararren masanin tarihi ne, ga abin da yake cewa dangane da kaburburan imamai (A.S) da suke a "bakiyya" yana cewa:

"A bisa kaburburansu a akwai dutse wanda aka rubuta: Da sunan Allah mai rahma mai jin kai, godiya ta tabbata ga Allah wanda yake kashe al’umma yake kuma raya matattu. wannan shi ne kabarin Fadima "yar manzon Allah (S.A.W) wadda take ita ce shugabar matan duniya. Da kabarin Hasan bn Ali bn Abi Dalib da kabarin Ali bn Husain bn Ali bn Abi Dalib da kabarin Muhammad Bn Ali Bn Husain bn Ali Bn Abi Dalib da Kabarin Ja’farus Sadik Bn Muhammad". [74]

Mas’udi ya kasance daga cikin masana tarihi na karni hudu Bayan hjira. ’Yan salafiya wadanda suke da kankamo sun tafi a kan cewa, wannan karni da karnonin da suke kafinsu su ne fiyayyun karnonin tarihin musulunci, sannan ayyukan da suka yadu a tsakanin musulmi a wannan zamani suna nuna kasantuwar abubuwan da shari’a ta yarda da su. Amma abin bakin ciki wannan babban dutse wanda Mas’udi yake fada wanda aka yi wannan rubutu a kansa, sakamakon rushewar da wahabiyawa suka yi wa "bakiyya" yanzu babu shi a samuwa. Saboda haka yanzu wadannan kaburbura ba a iya bambance su.

Ibn jubair[75] (540-614) shahararren mai yawo bude ido ya ziyarci kaburburan annabawa da bayin Allah a kasashen Misra, Makka, Madina,

Iraki da Sham, yayin tafiye-tafiyensa kuma ya yi bayani a kan kowane daya daga cikinsu a cikin littafinsa na tafiye-tafiye, ta yadda dukkammu zamu iya samun wannan a cikin wannan littafin nasa. Ta hanyar karanta wannan littafin musulmi suna samun masaniya a kan tarihin gina hasumiyoyi da gine-ginen kaburburan annabawa da waliyyan Allah. Dangane da abin da ya zo a cikin wannan littafin tafiye-tafiye nasa shi ne: Tarihin gina manya-manyan gine-gine a kan kaburburan Imamai da waliyyai da shahidai a tafarkin Allah, wanda yake komawa zuwa ga zamanin sahabbai da tabi'ai. Wanda yake nuna yadda a wancan zamanin da musulmai suke nuna kauna da kulawarsu dangane da shugabanni da manyan addini, ta yadda suka tashi domin gina wurare masu kawatarwa domin girmamawa gare su. Sannan babu wani daga cikin sahabbai wanda ya nuna cewa wannan aiki yana komawa ne zuwa ga shirka ko kuma ya saba wa tauhidi da kadaita ubangiji. Kamar yadda Ibn Jubair ya fara tafiyarsa daga gaban duniyar musulunci (Andulus) zuwa yammacinta ta yadda kasar Misra ta kasance wuri mafi kusa gare shi, Sai ya fara da wuraren tarihin da suke a Misra musamman Alkahira. Zamu kawo wasu daga cikin abin da ya rubuta daga cikin wadannan gine-gine na musulunci a wannan kasa:

## Gini Mai Girma Na Kan Imam Husain (A.S) A Alkahira

Wasu sun tafi a kan cewa an rufe kan Imam Husain (A.S) a garin Alkahira, saboda haka suka gina wani wuri da sunan "Ra'asul Husain" inda mutane suke zuwa ziyara daga cikin gida da waje. Masu sabon aure a wannan gari sukan je Masallacin Husain (A.S) wanda yake a wannan wuri sukan yi dawafi.. [76]

Ibn Jubair yana cewa: Daya daga cikin wurare masu tsarki a Alkahira shi ne Wurin da aka rufe kan Husain, an kawata wannan wuri da azurfa, wannan gini yana da girma da daukaka ta yadda harshe ba zai iya siffanta shi ba. A kan wannan gini akwai wani dutse na alfarma kai kace madubin Indiya ne, ta yadda yake haske yana dauko hotunan abubuwan da suke a gabansa. Yace: Da idanuna na ga masu ziyarar Husaini (A.S) yadda suke kuka suna sumbatar yadin da aka dora a kan abin da aka rufe kabarinsa da shi suna neman tabarraki suna addu'a, ta yadda kwallarsu kamar ta rufe wannan kabari.

Ibn Jubair ya ambaci wani wuri da ake kira "Karafa" inda yake cewa yana daga cikin wurare masu ban al'ajabi kamar yadda ya bayyana akwai kaburburan annabawa da iyalan Manzo da sahabbansa da tabi'ai da sauran kaburburan manyan malamai da aka rufe a wannan wuri. Dan Annabi Salih (Raubil) dan Annabi Yakub (Ishak) da matar Fir'auna dukkansu an rufe su ne a wannan wuri. Haka nan daga cikin iyalan Manzo akwai dan Imam Ja'afar mai suna kasim da dansa Abdullah bn Kasim da dansa Yahya bn Kasim, sannan da kabarin Ali bn Kasim bn Abdullah bn Kasim da dan'uwansa Isa bn Abdullah.

Ibn Jubair ya ambaci da yawa daga cikin 'ya'yan Ali (A.S) wadanda aka rufe su a can. Haka nan akwai kaburburan Sahabbai tabi'ai ba shugabanni kamar Imam Shafi'i ta yadda yake magana a kan girma da matsayin haraminsa, kamar yadda yake cewa: Salahuddin Al'ayubi shi yake biyan kudin da ake bukata domin gabatar da bukukuwa a wannan harami na Imam Shafi'i.

## Hasumiyoyi Masu Tsawo A Garin Makka

Ibn Jubair yana bayyana yadda garin Makka ya kasance da hasumiyoyi masu daukaka a kan kaburbura a garin Makka, wanda ambatonsu a nan zai janyo mu tsawaitawa. Akwai wurare kamar Maulidin Nabi, Maulidin Zahara da Darul Khaizaran (wurin ibadar Manzo na sirri). Sannan ya ambaci wurare masu girma na sahabbai da tabi’ai a Madina, A cikin wannan kuma yake ambatar Raudhar Abbas bn Ali bn Hasan bn Ali (A.S) wanda yake da gini mai tsayi a garin Madina, sannan ya cigaba da bayyana yadda wadannan wurare suke.

Idan muna so mu fadi duk abubuwan da Ibn Jubair ya gani a garuruwan Sham da Iraki na sahabbai da manyan bayin Allah zai janyo mu tsawaita a cikin hakan. Don haka muna iya wadatuwa da wannan. Saboda haka wanda yake so ya samu karin bayani sosai a kan haka sai ya koma zuwa ga wannan littafi nasa.[77]

IBn Najjar (578-643) [78]: Muhammad bn Mahmud wanda aka fi sani da Ibn Najjar wanda yake shi ma shahararren musulmi mai yawon shakatawa ne a cikin littafinsa "Madinatur Rasul" yana cewa: "Akwai wata dadaddiyar hasumiya mai tsawo a farkon makabartar "bakiyya" wadda take da kofofi guda biyu wanda kowace rana ake bude daya daga cikinsu domin masu ziyara.[79]

Wadannan suna daga cikin littattafan tafiye-tafiye da muka dauko daga cikinsu, sannan ana iya komawa zuwa ga wasu littattafai na tafiye-tafiye wadanda suke tabbatar da yin gine-gine a kaburburan annabawa da bayin Allah wani abu ne da yake sananne kuma wata Sunna ce mai tsawon tarihi a tsakanin masu kadaita Ubangiji.

Ibn Hajjaj bagdadi (262-392) wanda yake mawaki ne sharare a iraki ya yi wata kasida ta yabon Imam Ali (A.S), sannan ya yi wannan kasida ne a haramin Imam Ali (A.S) a cikin taron mutane, a farkon wannan kasida ga abin yake cewa: "Ya kai ma’abocin wannan hasumiya fara a garin Najaf duk wanda ya ziyarce ka kuma ya nemi ceton Allah daga gareka to Allah zai karbi cetonsa". Wannan baiti yana nuna cewa kabarin Imam Ali (A.S) a farkon karni na hudu ya kasance yana da hasumiya.

Abin mamaki a nan shi ne a mahangar ilimin Usulul fikh haduwar mutane a kan hukuncin wani abu har zuwa karnoni da dama yana nuna ingancin wannan abin ne. Amma musulmi sun hadu a kan ingancin gine-gine a kan kabarin annabawa da waliyyan Allah tsawon karnoni masu yawa, amma mahangar wasu wannan bai isa ya zama dalili ba, ta yadda kowane lokaci suna kokarin kaucewa a kan yarda da wannan al’amari.

## Gineginen Tunawa Da Bayin Allah Da Dalilai Masu Sabani A Kan Haka

Mun yi bincike a kan dalilan da suke nuni da ingancin ziyar da girmama kaburburan bayin Allah daga Kur'ani da Sunna da tarihin magabata, amma yanzu lokaci ya yi da zamu yi bincike a kan dalilan masu inkarin hakan. Wanda sukan yi riko da hadisin Abil Hayyaj Asadi ne a kan hakan, yanzu zamu auna wannan hadisi ta yadda zamu ga kimarsa ta hanyar ma'aunin da ake gane ingancin hadisi.

Muslim a cikin sahih dinsa yana ruwaitowa daga Abil Hayyaj kamar haka: "Ali bin Abi Dalib ya ce da ni: Ba na aike ba a kan abin da Manzo ya aika ni a kansa ba, kada ka bar wani hoto sai ka lalata shi, ko wani kabari mai tudu sai ka daidaita (baje) shi."

Masu adawa da wannan al'amari suna kafa dalili ne da wannan hadisin a kan haramcin gina haramin wani Imami daga cikin Imamai (A.S) sakamakon haka ne a shekara ta 1344Bh suka rusa makabartar "bakiyya" a wannan rana ne kuma a cikin jaridar "Ummul kura aka sanya tambaya da amsa dangane da dalilan da suka sanya aka rusa wannan makabarta, domin mu gane ta yadda aka kafa hujja da wannan hadisi yana da kyau mu yi bincike a kan ma'ana da kuma dangane wannan hadisi:

## A-Sanadin Wannan Hadisi

Maruwaitan wannan hadisi su ne kamar haka: 1-Waki 2-Sufyanus sauri 3-Habib bn Abi sabit 4-Abu wa’il 5-Abu hayyaj Asadi.

Dangane da maruwaici na farko kuwa abin da Ahmad bn Hambal wanda malamin hadisi ne yana cewa dangane da shi ya wadatar da mu inda yake cewa: Waki yayi kuskure a cikin hadisai guda 500, [80]Sannan ya cigaba da cewa: Ya kasance yana ruwaito hadisi da ma’ana (ba tare da kiyaye lafuzzan da aka yi amfani da su ba) Sannan ba shi da cikakkiyar masaniya a harshen larabci. [81]

Dangane da maruwaici na biyu kuwa (Sufyanu sauri) Ibn hajar Askalani ya ambace shi da cewa yana yin "Tadlis"a cikin hadisi. An ruwaito daga Ibn Mubarak cewa, Sufyanus Sauri ya kasance yana ruwaito hadisi yana yin "Tadlis"a lokacin da na iso sai ya ji kunya a kan abin da yake yi.[82] duk kuwa yadda aka fassara ma’anar tadlis ba ya dacewa da adalci.[83]

Dangane da maruwaici na uku kuwa, Habib bn abi Sabit, Ibn Hibban ya ruwaito daga Ata yana cewa: Ya kasance yana tadlis a cikin hadisi, don haka ba a bin hadisinsa, [84]

Amma mai ruwaya na hudu kuwa, wato Abu wa’il wanda sunan shi Shakik bn Salma Asadi Kufi, ya kasance abokin adawar Ali bn Abi Dalib ne, Ibn Abil Hadid yana cewa: Ya kasance daga cikin masu sabani da Imam Ali (A.S) Lokacin da aka tambaye shi Ali kake so ko Usman, Sai ya ce: wani lokaci na kasance Ali amma yanzu Usman.[85]

Sai dangane da maruwaici na biyar wato Abu Hayyaj Asadi wanda sunansa Hayyan bin Husain, Tirmizi yana kauce wa ruwaito hadisi daga gare shi, haka nan Ingantattun littattafan hadisai guda biyar ban da wannan ruwayar ba su ruwaito komai daga gare shi. [86]

## B-Dangane Da Ma’anar Wannan Hadisi

Dangane da kirkirar wannan hadisi na Abu hayyaj kuwa kamar yadda muka gani a sama a fili yake abin, domin kuwa maruwaita wannan hadisi ta yadda ake tuhumar su yin tadlis da kuskure wajen ruwaya. Saboda haka ba za a iya dogara da shi ba wajen kafa dalili na shari’a. Koda an runtse ido daga raunata maruwaita wannan hadisi, ma’anarsa ba tabbatar da wannan ma’ana. Saboda haka: domin bayyanar da wannan al’amari ta hanyar bayyanar da wasu kalmomin don fahimtar ma’anar wannan hadisi.

1-"Kalmar: Kabran musharrafan"

2-"Illa sawwaitahu"

Wadannan kalmomin sune suka zo a cikin wannan hadisi;

Dangane kalma ta farko zamu yi bayani ne a kan kalamar "musharraf" wadda take da ma’anar daukaka wato abu madaukaki. Don haka ne wadanda suke daga babban gida kamar iyalan Manzo ake kiransu da sharifai, Sannan tozon rakumi saboda kasantuwarsa yana da daukaka a kan sauran jikinsa ana kiransa da "Sharaf".

Ya zo a cikin Tajul Arus cewa: Sharaf ma’anarsa shi ne wani wuri mai tudu, wato madaukaki. Sannan ana kiran tozon rakumi da sharaf, Sannan wurare masu bisa kamar gidajen sarakuna ana kiransu da Sharaf, Haka nan akan kira tudun da yake a kan bangaye da wannan kalma.[87] Saboda haka wannan kalma tana nufin abu mai daukaka ko kuwa kawai tana nufin tozon rakumi ko bayan kifi?.

Tare da kula da ma’anar kalmar "Sawwaitahu" kamar yadda zamu yi bayanin a kanta zamu fahimci cewa wannan kalma ta Sharaf a cikin wannan hadisi tana nufin ma’ana ne ta musamman.

Dangane da kalma ta biyu kuwa muna iya bayani kamar haka: Kalma ta Sawwaitahu da ta zo da ma’anar aiki wato baje wani abu ko dai-daita shi, ana mafani da ita a cikin harshen larabci da ma’anoni guda biyu.

1-Daidaita wani abu da wani abu daban ta hanyar tsawo ko girma ko makamancin haka. Saboda haka idan da wannan ma’ana kalmar sawwa ta zo tana da aikau guda biyu (maf’ul) wanda a cikin harshen larabci wannan maf’ul na biyu yana bukatar harafin jarra wanda zai dai-daita wannan abin da waninsa.[88]

2-Ma’ana ta biyu kuwa shi ne baje wani abu ta yadda zai daidaita babu tudu da kwari, saboda haka a nan wannan fi’ili na sawwa yana bukatar maf’uli guda daya, ba shi bukatar na biyu. Saboda haka duk lokacin kafinta ya daidaita wani katako, kawai zai ce na goge katako, (wato sawwaitul khashab). [89]

Saboda haka bambanci wannan ma’anoni guda biyu a bayyane yake, wato a ma’ana ta farko siffa ce ta abubuwa guda biyu, amma a ma’ana ta biyu kuwa siffa ce ta abu guda (wato daidaita wani abu ba tare da an hada shi da waninsa ba kamar yadda muka gani). Saboda haka yanzu mun fahimci ma’anonin wadannan kalmomi guda biyu: wato "Sawwaitahu da musharrafan".

Saboda haka muna iya fahimtar cewa wannan hadisi yana magana ne dangane da yadda wannan kabari yake domin kuwa yana magana ne a kan abu guda, ba wai kabari ba da kasa (wato ba a daidaita shi da kasa ba wato a daidaita shi kansa kabarin) Domin da haka ake nufi sai a ce "sawwaitahu bil

ard". Saboda haka abin da Imam yake nufi a cikin wannan hadisi shi ne, duk inda ya ga wani kabari yana da tudu da kwari kamar tozon rakumi ya dai-daita shi ya gyara shi ya zama kamar dakali. Saboda haka wannan hadisi yana nuna mana yadda za a yi kabarin musulmi ta yadda za a baje samansa ba a yi masa tulluwa ba kamar bayan rakumi ko kifi.

Domin kuwa wannan zamani a kan yi kaburbura ne da tudu kamar yadda bayan rakumi yake, don haka ne Imam ya ba Abu hayyaj umarni da ya daidaita duk kabarin da ya gani a haka. Saboda haka wannan hadisi wace alaka yake da shi wajen rusa shi kansa kabari ko ginin da aka a samansa?!

Kuma cikin su maruwaitan wannan hadisi da masu sharhinsa sun bayyana ma'anar wannan hadisi kamar yadda muka yi bayani a sama.

1-Muslim ya ruwaito wannan hadisi karkashin babin "Amr bi taswiyatul kubur" wato ruwayoyin da suke magana a kan daidaita saman kabari, saboda haka muna iya cewa shi ma muslim abin da ya fahimta da ma'anar wannan hadisi kenan (wato kasantuwar kaburbura kamar yadda dakali yake ba kamar yadda bayan rakumi yake ba).

2-Muslim a farkon wannan babi ya ruwaito cewa: Fudhala tare da wasu mutane sun kasance a Rom, Sai wani daga cikin mutanensa ya rasu sai ya rufe shi ya yi kabarinsa kamar yadda ake dakali (Rectangle) sai ya ce haka na ji daga Manzo (S.A.W). ya ce: Ku yi kaburbura kamar haka wato samansu a baje ba tare da tudu ba.

Saboda haka dukkan wadannan hadisai suna bayyanar mana da ma'anar Kalmar Musharrafan da ta zo a cikin hadisi, ba tana nufin kasancewar kabari ya yi bisa ba daga kasa ko kada ya yi, tana nufin shi kansa kabarin kada ya kasance yana da tudu kamar bayan rakumi.

3-Nabawi kan sharhin wannan hadisi yana cewa: Bai kamata ba kabari ya yi bisa da kasa ba ko kuma ya zamana ya yi tudu kamar bayan rakumi. Ya cigaba da cewa dole ne bisansa ya kasance kamar kamun hannu guda sannan samansa ya zamana a baje ba mai tudu ba. [90]

4-Kurdabi a cikin tafsirinsa ya ruwaito wannan hadisi da aka ambata yana cewa: Wannan hadisi abin yake nunawa shi ne baje kabari shi ne Sunna, sannan yi masa tulluwa bidi'a ne.[91]

5-Ibn Hajar askalani bayan ya yi bayani a kan mustahabbancin baje saman kabari yan rubuta cewa: Hadisin Abi Hayyaj ba yana nufin cewa ba a baje ya zama daidai da kasa, abin da yake nufi shi ne a baje saman kabari ta yadda za a daidaita shi babu wani tudu a samansa, duk da yake cewa ya dan yi sama da kasa.[92]

Kamar yadda wasu ba su ba wannan bayani muhimmanci ba, (mu dauka ma wannan hadisi yana nufin cewa a baje kabari ta yadda zai zama daya da kasa babu wani tudu) kafa hujja da shi a kan rusa gine-ginen da aka yi a kaburburan bayin Allah, zai fuskanci matsaloli guda biyu:

1-Baje kabari ta yadda zai zama daya da kasa babu wani tudu ya sabawa dukkan ra'ayin fukaha domin kuwa dukkansu sun tafi a kan haka din cewa mafi karanci tashinsa ya kai kamun hannu guda.[93]

2-Idan muka dauka cewa wannan hadisi yana nufin cewa a baje kabari ta yadda zai zama daidai da kasa, to dole ne mu rusa kabari ta yadda zai zama daya da kasa, ba wani gini da aka yi ba a saman kabarin. Saboda haka sam

wannan hadisi ba yana magana ba ne a kan ginin da yake kan kabari yana magana ne a kan shi kansa kabarin!.

Godiya ta tabbata ga Allah wanda ya yi umarni da girmama annabawa da wasiyyansu.

# Abin da Littafin Ya Kunsa

## Abin da Littafin Ya Kunsa

1 ....................HIKIMAR ZIYARAR KABURBURAN WALIYYAI
1 ............................ Wallafar: AyatulLahi Sheikh Ja'afar Subhani
1 .........................................Fassarar: Yunus Muhammad Sani
1 ........................................Dubawar: Hafiz Muhammad Sa'id
2.......................................................Ziyarar Kaburbura Masu Daraja
3...........................................................Ziyartar Kaburburan Masoya
4.......................................................... Ziyarar Kaburburan Malamai
5...........................................................Ziyarar Kaburburan Shahidai
6......................................................Ziyarar Kabarin Manzo (S.A.W)
8.....................Ziyarar Kabarin Muminai A Mahangar Kur'ani Da Sunna
9............................................ Ziyarar Kabari A Cikin Sunnnar Manzo
10 .................................................................. Mata Da Ziyarar Kabari
12 ..................................................Amsar wasu tambayoyi guda biyu
Ziyarar Kabarin Manzo Mai Girma A Mahangar Malaman Hadisi Da
14 ............................................................................................ Fikihu
17 .......................Ziyarar Kabarin Manzo A Mahangar Kur'ani Da Sunna
20 ........................................Ziyar Manzo A Ruwayar Ahlul-Bait (A.S)
21 .................. Tattaunawar Imam Malik Tare Da Mansur Dawaniki
22 ......................................................Ziyarar Kabari Da Kiyaye Asali
24 .................................Tafiya Domin Ziyarar Kabarin Manzo (S.A.W)
26 ..............................Masu Haramta Tafiya Don Ziyarar Manzo
28 ......................................................Ziyarar Masallatai Guda Bakwai
29 ..................................................Girmama Kaburbura Masu Tsarki
Kaburburan Shugabannin Addinin Musulunci Suna Nuna Tarihin
31 ....................................................................................... Musulunci
33 ...........................................................Daukar Darasi Daga Tarihi
35 .................................. Matsayin Gidajen Annabawa A Cikin Kur'ani
39 ............................................ Soyayyar Manzo (S.A.W) Da Iyalansa
41 ........... Kaburburan Manzanni Da Tarihin Magabata Ma'abota Tauhidi
43 .....................Gini Mai Girma Na Kan Imam Husain (A.S) A Alkahira
44 ....................................... Hasumiyoyi Masu Tsawo A Garin Makka
Gineginen Tunawa Da Bayin Allah Da Dalilai Masu Sabani A Kan Haka
45
46 ............................................. A-Sanadin Wannan Hadisi
47 ................................B-Dangane Da Ma'anar Wannan Hadisi
50 ........................................................... Abin da Littafin Ya Kunsa